[1/26, 10:59 PM] Matar Malam: 💫
*41&42*
Shigowar mahaifyarta d'akin ne ya katse tunaninta, cikin mutuwar jiki ta tashi zaune ta tana kallonta har ta k'araso ta zaune gefen gado babu walwala a fuskarta.

A d'an raunane tace."Mamnah barka dare." Tana nazarinta ta amsa da fadin." Barka dai me yake damunki ne baki fito kin ci abinci ba."? Kamar me jiran kiris sai kawai ta fara share hawaye murya a sarke tace."Mammah ya za'ayi na iya cin abinci a irin wannan halin, gabadaya kun kasa fahintata kuna nema ku jefa rayuwata a cikin masifa, yanzu tsakani da Allah a gidan nan wa aka ta'ba yiwa auran dole acikin 'yan uwana, kowacce fa wanda takeso aka aura mata amma ni an d'auke ni kyauta an bawa wani wanda bashi da cikakken asali wallahi ba'ayi min adalci ba."

Ta dinga kallonta tana tunano wani lamari daya shud'e shekaru masu yawa, Ajiyar zuciya ta sauke kafin tace." Yanzu Ke a ganinki hakan da akayi miki rashin adalci ne." ? shuru tayi ba tace komai ba, ta cigaba da cewa." Ke ba kiji kunyar fadin wannan maganar ba? shin wai to ya kike so ayi miki da har kike fadin ba'ayi miki adalci ba, ai na dauka sai da aka baki lokaci domin fita hakkinki me yasa baki fitar da mijin aure ba, ko kuma kin fiso kiyi ta zama a haka babu aure mutane na zarginki."?

Girgiza kai tayi da fadin" Mammah sati biyu yayi kadan, har yaushe na dawo na samu nutsuwa komai fa yana bukatar nutsuwa da kwanciyar hankali, amma sai kawai a yanke min hukuncin da bai cancanta ba, gaskiya ni ba'ayi min adalci ba don banga abunda zanyi da wannan ba'kauyen mutumin ba."

Murmushi mai ciwo tayi kafin tace." Wannan ba'kauyen da ki ka raina shine marufar asirinki domin a halin yanzu idan bashi din ba babu wanda zai aureki ki samu zaman lafiya saboda haka ki kiyaye ni wallahi, kada na kara jin kin furta wata mummunar kalma akan wannan al'amari, idan ban da butulci ma irin naki wannan yaron ai bai cancanci haka daga gurinki ba."

Hawaye ta goge da fadin." Ni dai kawai bana son shi ne ko kadan a raina domin ba tsaran aura ne bane, amma shikkenan tunda kun gaji da zama dani zan aure shi kamar yanda kuke so sai duk abunda ya biyo baya kada kuyi kuka dani."

Cike da mamaki! take kallonta kafin tace." Zaki caka masa wuka ya mutu kenan."?

Girgixa kai tayi tana share hawayen dake zuba a saman fuskarta.

Taja dogon tsaki da fadin "Karshen k'iyayye dai ki caka masa wuka a mak'oshi! ko kuma ki zuba masa guba a abinci ya mutu! to idan baki fasa aikata daya daga cikin wannan ba bakya kaunar Allah da Annabi, wallahi ki ka kashe shi kema sai an kashe ki! kina ta'kamar gata ko? ubanki yana da kudi da mulki idan kin kashe rai yana da abunda zai fanshe ki, to bari kiji

wallahi nayi miki rantsuwa da Allah ki ka kashe rai! sai na tsaya kai da fata kema kin fuskanci hukunci dai-dai da abunda ki ka aikata! idan wannan ne kud'irinki akan UMARU to kada ki fasa."
Tana gama k'are maganar ta tashi ta fita daga dakin ranta a b'ace! al'amarin yarinyar yanzu tsoro yake bata, dole ta tsananta da addua akan al'amarin.

Bayan fitar ta daga dakin komawa tayi ta kwanta hawaye na bin gefen fuskarta, ita ba nufin ta kenan ba, kawai ta fadi abinda yake cikin zuciyarta ne, bata fatan kashe kiyashi ballantana wani dan adam.

Bacci rabi da rabi tayi saboda tsabar damuwa.

Da asubar fari ta kira wayar Asp dama duk tana da numbers su. A lokacin data kira wayar dawowarsa kenan daga massallaci, ganin sabuwar number besa shi mamaki ba, wayar yasa a kunnansa da sallama a bakinsa.

Murya a dashe ta amsa kafin ta gaisheshi.

Sai ya shiga tunanin inda ya san muryar don dashewar ta sanya ya kasa tantance muryarta.

"Wacece ne bangane mai magana ba."?

Hanci taja ta dan sake bude muryar da fadin." ZINAT ce."

Gabansa ya fadi kadan, yace." Zinatu kece ashe ina fatan dai lafiya."?

"Numfashi ta sauke kafin tace."Ai kai ma tunda kaga wannan kiran kasan ba lafiya ba."
Tafad'a cikin dusashewar murya.

Lokaci guda ya harbo jirgin, gefen gado ya zaune da wayar a makale a kunnansa yace." To menene kiyi min bayani Ina jinki."

"Asp me yasa za'a hada baki da kai a cuci rayuwata."? cikin sigar tuhuma take tambayarsa

Yace." Bangane maganarki ba." Ajiyar zuciya ta sauke da fadin." Ba zaka gane ba tunda bakinku daya amma ina so ka sheda masa cewa ni ba tsaran auransa bace idan yana farin ciki da dariya to ya dena domin aure na zai zame masa tashin hankali."

Da sauri yace."Subahanallahi! Zinatu duk me ya janyo wannan maganar."?

Tayi saurin tare shi da fadin."Ni dai sako na baka, ka fada masa cewa bakin rijiya ba gurin wasan makaho bane."

Maganar sai ta bashi dariya, ya d'an dara kafin yace." Aa ni wannan maganar bana cikinta amma bari na baki number sa sai ki fada masa baki da baki."

Tace."Ai ba tsoronsa nake ba turo min number. " Yace."Yanzu kuwa." Kashe wayar yayi yana mamakin al'amarin, gaskiya akwai matsala babba.

Kafin ya tura mata number sai da ya kira shi ya sheda masa abunda ke faruwa yace." Don Allah kada ki biye mata ku lalace gabadaya na fahimci rarrashi take bukata, ka rarrasheta kada ka kara mata wani takaicin."

Dariya kawai yayi kafin ya amsa masa da "to shikkenan zanyi yanda kace din." Yaji dadin hakan sosai domin shi haka kawai yake so yaga tabbatuwar auran.

Yana tsaka da shiryawa ta kira wayar, da yake Asp ya bashi numberta koda ya duba yaga itace sai ya share yaki dagawa.

Sai da ta kira sau uku sannan ya daga babu wargi yayi sallama.

Ba tare da ta amsa ba cikin gadara da fitsara! tace. Kana jina ko."?

Shuru bece komai ba, taja dogon tsaki! da fadin." Nasan a halin yanzu kana nan cikin murna da farin ciki da samun abunda ba kayi tsammani ba, to bari kaji wani abu farin cikin ka zai zama bakin ciki! haka zalika dariyarka zata zama kuka domin daga ranar da akace an d'aura mana aure zaka gane cewa kayi tsaurin ido! na bawa abokinka sako yace sai da ya bani number ka, nace ya bani domin bana tsoron sheda maka abunda yake zuciyata."
Ta'kare maganar tana numfarfashi!

A nutse yace." Kin san macen da ake kira da (Matar ladan noma."?) shuru tayi tana nazarin sunan.

Yace."Tunda baki gane ba bari na ganar dake, mahaifinki ya bani kyautarki sadaki kawai zan bayar, ban ta'ba jin sonki a raina ba, domin baki ma da abinda zaki ja ra'ayi na, ina da wacce nakeso yarinya mai kyau mai hankali nutsuwa da tarbiya ke kam (Matar ladan noma ce) banyi noma ba, amma taimakon da nayi miki yasa mahaifinki ya bani ke ni kuma na kar'ba saboda kada na watsa masa k'asa a ido, zan zauna zaman aure dake ba don ina sonki ba."ya kare maganar hankalinsa kwance.

Bakinta ne ya mutu murus! bata tsammaci ya iya cin mutunci haka ba, ta kasa ce masa komai sai wata irin zazzafar ajiyar zuciya da take sauke masa a kunne.

Cikin rashin damuwa Yace."Zan kashe waya idan baki da magana."

Da 'kayar ta iya danne kukan bakin cikin da yake kokarin kufce mata tace." K'azami bagidaje ba'kauye kawai."!
Tayi saurin kashe wayar ta jefar saman gado, zaman 'yan bori tayi kasan kafet taci kukanta ta koshi. kalmar ce kawai take mata amsa kuwwa a kunne *Matar ladan noma!* lallai in baki ya san abinda zai fada to be san abunda za'a mayar masa ba.

Sam maganganunta basu bata masa rai ba, hankalinsa a kwance ya cigaba da shirye-shiryensa, besa damuwarta a ransa ba tunda ya riga ya san dole hakan zata faru, yasan cewa akwai jan aiki a gabansa, amma hakan be daga masa hankali ba ya riga ya shirya ya kuma tanadi hanyoyin da zai bi cikin ruwan sanyi yayi maganinta.

***

Tafi sati biyu tana jinyar kanta, tare da bakin cikin ba'kaken maganganunsa! duk sanda zata tuna sunan daya kira ta dashi sai tayi kukan takaici (Matar ladan noma) wannan sunan yakan sanya duk wani alkadari nata ya karye duk shirin da tayi a kansa daga zarar ta tuna cin mutuncinsa sai jikinta ya mutu! gabadaya ta rasa yanda za tayi da rayuwarta gashi ta kasa gane kan mahaifiyarta fushi take da ita sosai! hakan ya k'ara daga mata hankali mutuka, dole haka ta sanyawa zuciyarta dangana ta aro walwala da farin cikin tasa a cikin ranta ta nuna sadudarta a zahiri. sannan har dakinta taje ta nemi afuwarta akan furucin da tayi a kwanakin da suka wuce.

Ganin yanda ta saki ranta tana walwala da farin ciki sai itama ta sakar mata fuska ta fara janta a jiki tana yi mata nasiha tare da nuna mata yanda rayuwa take gefe guda kuma tana gyara mata jiki da magungunan mata masu kyau da inganci.

Hakuri kawai tayi ta daure zuciyarta take amfani da kayan matan, duk dan ta nuna mata cewa ta hakura da auran kuma babu wani mummunan kudiri a cikin zuciyarta. .........Hakan da tayi sai tasa 'Yan uwanta farin ciki dama kullum adduarsu Allah ya shiryi ta ta gane hanya me kyau.

Tun ranar data kira shi a waya yaci mutuncinta bata sake kuskuran 'kara kiran sa ba saboda tana gudun ya kuma dan'kara mata wata mummunar maganar.

A nasa bangaran shima be tsammanci kiran nata ba harkokin gabansa kawai yake, ya manta da ita da lamarinta, shirye-shiryen tafiyarsa training yake, sai dai be manta da adadin kwanakin da suka rage a d'aura auran ba.

A daran ranar da zai tafi suke tattauna maganar da Asp yace." UMARU tafiyarka training ba zata hana faruwar komai ba, meye amfanin abotarmu ni zan tsaya maka akan komai kuma zan wakilce ka, sannan kuma ni ne zan bada sadaki domin a gabatar da komai anyi hakan ba

daya ba kuma sau biyu rashin hallatarka d'aurin auran ba zai hana ace aure be d'auru ba, saboda haka ka kwantar da hankalinsa insha Allah sai dai kawai ka dawo ka samu amaryarka na jiranka." Cikin zolaya ya 'kare maganar.

Murmushi yayi tare da sauke ajiyar zuciya Yace." Nagode sosai mutumina Allah ya saka da alkairi ya kuma bar abota da amana."

Ya amsa da "Ameen ya Allah amma yana da kyau kafin ka tafi ka shedawa mahaifin yarinyar halin da ake ciki koda ta waya ne."

Yace."Eh dama ina da tunanin hakan, a daran nan zan kira shi mu tattauna maganar."

Ya bashi hannu da fadin."Hakan yayi Allah yasa ayi sa'a." Ya amsa da ameen ya Allah abokina.

To koda ya shedawa Maimartaba Omar halin da ake ciki sai shima ya nuna masa cewa hakan ba wani abu bane, kamar yanda Asp din ya tabbatar masa da cewa ana yin hakan ba matsala bace mutukar akwai wakilinsa shikkenan magana takare, ya kuma karfafa masa gwiwa tare dayi masa kyawawan adduo'i.
Cikin mutunci da karamci sukayi sallama da juna...........Mutunci da dattakon dattijon yana mutukar burgeshi wannan dalilin ne kadai yasa har ya amince da auran yarinyar, tabbas da babu wannan bega dalilin da zai sashi auran mace mara nutsuwa da tarbiya irinta ba.

*Kika futar min da littafi keda Allah! ki ka karanta baki biya ba kema keda Allah!*

*#500via.....0542382124.....Binta umar gtbabk, idan kati zaki turo kiyi min magana ta WhatsApp da wannan number.... 07084653262.....BINTA UMAR ABBALE*
[1/27, 5:10 PM] Matar Malam: *43&44*
*GSR*
A daran ranar dai zai yi tafin ya samu Uwale da maganar domin su tattauna, ya sheda mata duk abunda yake faruwa ya kuma tabbatar mata da cewa halin da ake ciki a yanzu saura sati biyu kacal a daura auran, saboda haka ta shedawa duk wanda ya dace acikin 'yan uwa da abokan arziki.........Sosai tayi farin ciki da al'amarin dama shi aure lokaci ne gashi lokacin da ba suyi tsammani ba Allah ya nufa , sai dai kuma bata bar shi ya tashi ba sai da tayi masa maganar Hamra'u da yanda za'ayi da al'amarinta.

Yace."Uwale Hamra'u itace za'bi na kuma har yanzu ina sonta, aure na da wannan yarinyar ba zai hana na aureta ba, wannan auran yazo min bagatatan cikin rashin shiri, insha Allahu itama zan aure ta idan na samu nutsuwar da nake bukata.

Ta kalleshi da fadin." UMARU idan fa baka auri yarinyar nan ba ka yaudareta sai Allah yayi mata sakayya domin dai kai kanka kasan tuntuni  kai take jira kuma da bakinka kayi mata alkawarin aure kasan dole idan ta samu wannan labarin ta shiga damuwa tare da iyayenta don Allah kada ka bani kunya UMARU kada ka raba zumuncin da yake tsakanina da mahaifin yarinyar nan."

Ajiyar zuciya ya sauke kafin yace."Uwale kin san fa komai nufi ne na Allah,  mutum kan iya tsara rayuwarsa amma Allah sai  ya sauya masa,  mahaifin yarinyar nan yafi karfin komai a gurina dalilin kenan da yasa na karbi kyautar da yayi min, na kuma fada miki cewa hakan ba yana nufin na janye auran Hamra'u ba, zan aure ta da yardar Allah saboda haka ki kwantar da hankalinki itama yarinyar ki taushi zuciyarta."

Tace."To shikkenan UMARU Allah ya tabbatar da alkairi amma kafin ka tafi ka samu yarinyar ka sheda mata abunda yake faruwa kamar yanda kayi min bayani."

Agogon dake hannunsa ya duba, sha d'aya shaura na dare, yace." Ban 'ki  maganarki ba, zan sameta mu tattauna maganar  ko ba yanzu ba tunda yanzu dai dare yayi watakila tayi bacci." Tace." To shikkenan Allah ya kai ka lafiya ya kuma dawo da kai lafiya." Ya amsa da "Ameen ya Allah." Sallama yayi mata ya nufi wajensa.

Da Asubah bayan sun fito daga massalaci suka tsaya suna sake tattauna maganar,  Asp din yace."Naga tunda aka fara maganar auran nan ba kayi maganar lefe da sauran abubuwan bukata ba, kasan yarinyar nan fa 'yar rigima ce yana da kyau a rarrasheta ta wannan hanyoyin.

Yace."Asp ban san me yasa kake jin  tsoro da shakkar yarinyar nan ba, mahaifinta  fa kyauta ya bani ita sadaki kawai zan bayar to akan me zan takurawa kaina saboda ina gudan rashin kunyarta."

'Yar dariya yay da fadin." UMARU har yanzu ba'ayi macan da zata tsorata ni ba,  kawai dai ina nuna maka yanda za'ayi ka zauna da ita lafiya ne idan kana mata butsu to ba zaku ta'ba samun zaman lafiya da juna ba, maganar lefe kuma abunda ya dace ne koda kyauta aka baka kai kuma  sai ka duba cancanta da abunda ya dace."

Yace." A yanzu dai bani da kudin had'a mata lefe  sai dai idan tazo daga baya nayi mata."

Asp din ya dinga kallonsa yana mamakin furuncinsa,  wai bashi da kudi bayan irin tarin miliyoyin da yake dasu account ko sati biyu ba'ayi ba daga can abuja mai girma shugaban kasa yayi masa kyautar manyan kudi da dan'kareriyar mota harda gida a garin abujan amma shine yake maganar rashin kudi.

Girgiza kansa kawai yayi da fadin." UMARU wato abunda dai kayi ra'ayi shi kake ba'a baka shawara ka d'auka to ai shikkenan."

Yanda Asp din yayi maganar da b'acin rai a tare dashi yasa jikinsa sanyi ya bashi hakuri da fadin." Afuwa abokina ba wai naki daukar shawararka bane akwai dalilina na yin hakan, amma na janye domin farin cikin ka,  yanzu nawa zan bayar ayi lefen tunda kaga ni yau zan bar gari sannan kuma  ban ma san yanda ake hada lefen ba.

Yace."Ai magana ta wuce ko  sisin ka bazan kar'ba ba, lefe kuma ba za'a fasa ba, zan bawa madam kudi ta shiga kasuwa ta had'a duk abunda ake bukata."  Yana gama maganar yayi tafiyarsa.

Murmushi kawai yake yana binshi da kallo har ya k'urewa ganinsa, tunda Allah ya had'asu yake nuna masa 'kauna da sadaukarwa Asp ya zame masa dan uwa na jini, yanda yake sonsa da kaunarsa shima haka yake kaunarsa saboda duk wasu alkairai yayi masa kuma duk wani mataki da yake kai yanzu dalilinsa ne da jajurewarsa, hakika bashi da wani abu da zai saka masa dashi face addua.

*****

To kamar yanda Asp din yayi wa kansa  alk'awari sai da cika, don kudi masu yawa ya fitar aka had'a lefe dasu akwatina goma sha biyu cike da kaya set din gold har uku kuma duk masu nauyi, da yake da akwai fahimta a tsakaninsa da matansa babu wacce ta daga hankalinta, sai dai kuma sa'bani ya kusa giftawa a tsakaninsa da yarinyar da zai  aura a matsayin ta uku , al'amarin ya dinga bashi mamaki yana tunanin a inda ta samu labarin Zinatu da har take kishi a kanta, ganin yanda ta tashi hankalinta ne yasa ya zauna yayi mata bayani cewa yarinyar da abokinsa zai aura ce, dalilin da yasa ya tsaya akan al'amarin shi abokin  nasa baya gari yayi tafiya shiyasa ya tsaya masa akan al'amarin auransa." Wannan bayanin da yayi mata yasa ta kwantar da hankali amma da tayi tunanin ko yaudararta zaiyi.

Tun ranar da aka kai wa Uwale kayan lefen domin tasa albarka, Hamra'u ta  shiga tashin hankali mai tsananin gaske,  domin kasa zaman falon tayi ta shiga daki ta rufe kofa ta dinga rafsa ihu! bakin ciki da bakin kishi kamar ya kasheta.

Uwale ta shiga dakin ta sameta cikin mummunan yanayi, ta zauna tana rarrashinta gabadaya itama zuciyarta ta karye da al'amarin anya kuwa UMARU ba yaudararsu yake ba? a tunaninsu duk shine ya fitar da kudi masu nauyi aka had'a lefan, al'amarin dai duka bai musu dadi ba, ace ayi ta abu d'aya sai kace cin k'wan makauniya.

Tana kuka tace."Ashe Uwale har dake za'a had'a baki  a tozarta ni! me nayi miki kika tsanani har ki ka bada goyon bayan auro wata bayan gani, kin san kuma tsayin shekarun dana dauka ina jiransa, me yasa zaku ci amanata."

Hawayen tausayinta ta share kafin tace." Hamra'u ashe duk abunda yake faruwa UMARU be fada miki ba.?

Ta girgiza kai da fadin." Ni be fada min komai ba kuma kema ai be kamata ki 'boye min ba, yana da kyau duk abunda yake faruwa ki sanar dani nasan matsayina."

Tace."Hamra'u kada ki zarge ni ko kuma kiga laifina akan wannan al'amari, wallahi ni kaina ban san da maganar ba sai ana i gobe zai yi tafiyar nan yake sheda min halin da ake ciki, kuma ya tabbatar min da cewa wannan auran da zaiyi ba zai hana ya aureki ba, al'amarin ne yazo a k'urace shiyasa kuma kinga mahaifin yarinyar nan babban mutum ne wannan shine dalilin da yasa beyi jayayya dashi ba, a yanda na fahimtashi shima Auran zeyi shine saboda ganin mutuncin mahaifin yarinyar saboda haka ki kwantar da hankali UMARU ya tabbatar min da cewa kece za'bin sa kuma zai aureki da ikon Allah."

Ajiyar zuciya ta sauke tana jin sassauci a cikin zuciyarta, idan ta fahimci maganganun Uwale suna nuna mata cewar zai yarinyar ne saboda mahaifinta, ba wai dan yana sonta ba, wannan dalilin shi kad'ai sanya zuciyarta yin sanyi, amma dai duk da hakan ba zata hakura ba sai ta sake jin matsayinta a gurinsa.

******

Tsakanin Madam da Aunty Zeey amaryarta basa shiri sosai fad'a suke da juna, dalilin da yasa ma kenan basa iya haduwa guri daya domin mutukar suka hadu to sai sa'ba ni ya gifta a tsakaninsu, kuma ba kowa ke janyo rikicin ba sai Aunt Zeey maca ce mai bala'in kishi da ganin ido, ta tsani Madam da 'ya'yanta don dai ita ma Madam din a tsaye take shiyasa take shakkarta amma dai duk da haka idan sa'bani ya gifta a tsakaninsu sai sun buga, duk da ita Madam din tana kokarin ganin ta kama girma da mutuncinta.

To wannan dalilin yasa Asp din be gayyaci ita Aunty Zeey gurin zuwa kai kayan lefen ba, sai kawai ya bukaci mutane biyu daga b'angaran Uwale da wasu daga cikin 'yan uwansa da ita Madam din da Nabila yace suje su kad'ai ya isa.

Hakan yayi wa Aunt Zeey din ciwo, domin ita babban burinta ta 'kulla abota da amaryar tunda taji an ce 'yar sarauta ce take san k'awance da ita dama kuma tana kishi akan cewa duk matan abokan mijin nasu kawayen madam ne, wannan dalilin yasa takeso tayi kwace Zinat din domin samun abokiyar shawara.

Kasa hakuri tayi da abunda yayi mata ta kira shi a waya tana masa 'korafi akan me yasa zai mata haka, ai itama matarsa ce me yasa komai zai faru Madam ce a kan gaba ita gaskiya ta gaji da wannan abu, da yake yasan halinta sai ya rarrasheta da fadin shi beyi hakan da wata manufa ba, amma tunda ya fahimci tana so tayi abota da amaryar to idan ya dawo zai bata number ta sai su dinga gaisawa, hakan yayi mata dadi sosai tayi masa fatan dawowa lafiya.

Babu wanda be yaba da kayan lefen ba, domin 'karshen isa da kasaitar mace kenan, kaya ne da aka kashe iyayen kudi gurin had'awa tun daga kan kayan shafe-shafe har kan under wears

babu  na Najeria takalma da jakkunansu sunfi kala ashirin, bayan manya manya atamfofi da lesuka da iyayen shaddudi da goyayen riguna na waje da mayafai masu asalin kyau da tsada, fashion na sarkoki kam ba zasu lissafu ba bayan gold din dake cikin akwatinsu set uku,  kaya tamkar za'a bude sabon kanti..................Kowa ya yaba da kayan amma ban da ita, bata  fito ta nuna hakan a zahiri ba, sai dai har hazar yau da kayan sukayi kwana uku a gidan ba ta duba taga meye a ciki ba, tana kallon dai 'yan uwanta suka d'ibar mata wasu daga ciki zasu bayar a dinka mata,  shuru kawai tayi saboda bata so tayi wata magana su samu sa'ba ni da juna, suna ta murna da farin ciki gefe guda kuma suna shirye-shiryen yanda za'a gudanar da shagalin biki, ita dai ido ne nata duk abunda sukayi daidai ne, ta danne komai a ranta taki ta nuna musu zahirin abinda yake cikin zuciyarta.

Aunty Zeey sarkin shishshigi da iya waje sai da ta san yanda tayi ta samu shiga a gurinta, ta waya suka k'ulla abota, kullum sai sun gaisa da juna, wani sa'in har ita aunty Zeey din take dan bata labarin wasu abubuwan da suka shafeta da mijinta da kuma kishiyarta.......Tayi ta mamakin al'amarin, wani lokacin  idan taji tana zagin Madam da 'ya'yanta  ta kanyi mamaki! Tace." Ni kam kinga na zauna da matar amma ban ta'ba ganin mugun halinta ba.

'Kwafa take da fadin." Don ba kishiyarki bace shiyasa  amma ki san irin zaman da za kiyi da ita kuma kada ki dinga sakin jiki kina fad'a mata sirinki."

Dariya ta kanyi a duk lokacin da sukayi irin wannan maganar ta kanyi  mamakin yanda mata suke kishi akan namiji  ita kam duk irin so da kaunar da takewa namiji ba zata lalace guri kishi a kansa ba, a ganinta kishin da ake a kansu shine yake sawa suna iskanci yanda ransu yake so, shiyasa ita da namiji babu mutunci.

Aunty Zeey ita ta maye gurbin aminiyarta Sakina  wacce  ta tafi yawan siyasa sai dai duk abunda yake faruwa tana samun labari daga bakin k'awar tata, tana sa ran dawowarta kafin d'aurin auran.

*Kika futar min da littafi keda Allah!  ki ka karanta baki biya ba kema keda Allah!*

*#500via.....0542382124.....Binta umar gtbabk, idan kati zaki turo  kiyi min magana ta WhatsApp da wannan number.... 07084653262.....BINTA UMAR ABBALE*
[1/29, 10:25 PM] Matar Malam: 🍒
*45&46*
Hamra'u duk irin bayanin da Uwale tayi mata besa ta hakura ba ta kwantar da hankalinta ba, mugun kishin Zinatu take, gabadaya ta kasa samun nutsuwa da kwanciyar hankali,  gani take mutukar ya auri 'yar sarauta   to maganar auranta dashi zai sha ruwa,  da ta gaji da wasiwahsi da zuciyarta sai kawa ta yanke shawarar kiran wayarsa domin taji a matsayinta a gurinsa  duk

da cewa tunda ya tafi tsayin sati biyu da kwanaki goma be nema ta ba ballantana ya kira wayarta yaji ya take. Sai dai sa'i da lokaci ya kan kira Uwale su gaisa itama ba kullum ba, ita Uwalen ke bata sak'on gaisuwarsa gare ta, gashi kullum kara sonsa take da kishinsa, sam ta tsani wata mace ta kusance shi, gashi daj shine da bakinsa ya furta cewa yana sonta zai aureta amma duk wasu hanyoyi na nuna kauna da so da kulawa baya nuna mata, yanda ta lura kamar yafi bawa aikinsa muhimmanci a kanta.

Ta kira wayar tasa gabanta na dan fad'uwa! dalili bata san irin kar'bar da zai yi mata ba.

Koda yaga kiran nata beyi mamaki ba, sai da ya fita daga cikin jama'a sannan ya samu sararin amsawa.

Murya a sanyaye ta gaisheshi tana langwab'ewa! ya amsa cikin kulawa da fadin." Ina fatan duk kuna nan lafiya aiki ya hana ni samun sukunin kiran wayar ku mu gaisa, ina fata dai kina samun sakon gaisuwata a gurin Uwale."?

Zazzafar ajiyar zuciya ta sauke murya na rawa tace." Eh tana fada min a duk sanda ku kayi waya, amma yaya na me yasa ni ba za ka kira waya ta domin mu gaisa ba sai dai ka bada sa'ko."

Rashin abun fad'a yasa yace." Bana samun lokaci ne kullum cikin aiki nake wannan shine dalili amma kada ki damu har yanzu kina nan a cikin zuciyata."

Girgiza kanta tayi da fadin." Ina kokwanto akan maganar ka domin na samu labarin duk abunda yake faruwa wanda ka boye min zaka auri 'yar sarauta wannan ne dalilin da yasa kake kokarin ka juya min baya."

K'aramin tsaki yaja ya dan girgiza kai da fadin." Idan wannan ne tunaninki to ki daina domin ni ba a haka nake ba, aurena da Zinatu Allah ne ya kaddara! ban ta'ba tunanin had'uwa da ita ba, ballanatana har naji sha'awar auranta a raina, mahaifinta ne ya bani ita dalilin taimakon da nayi mata, babban mutum ne mai mutunci da dattako wannan dalilin yasa na kar'bi auranta domin yafi karfin alfarma a gurina."

Cikin jin sassauci sakamakon maganganunsa tace." To shikkenan ni yanzu na kira kane domin naji matsayina a gurinka."

Kansa ya dafe cikin rashin san damuwa yace." Wai shin Hamra'u sau nawa ki ke so kin san yaya matsayinki yake a guri na? na fada miki cewa ina sonki kuma ina da bukatar auranki saboda na yaba sa kyawawan halayenki wannan shine babban dalilin daya ja ra'ayi a kan ki, duk wasu kyale-kyale basa burgeni nagarta nake nema, amma duk da wannan bayanin da nayi miki na fahimceki kina kokwanto aikana shin me kike nufi ne."?

Dan murmushi tayi kafin ta kwantar da murya da fadin." Kayi hakuri Yayana bana nufin komai sai alkairi, na fahimce ka  kuma na amince da maganarka amma don Allah ka dinga nuna min kulawa sannan kuma tun kafin amaryar taka ta shigo gidanka ka sheda mata maganata domin ta san da zamana a zuciyarka."

Maganarta ta bashi haushi da mamaki! Yace." Okey kina so ki tsara min yanda zanyi kenan."? Yanda yayi maganar cikin shan mur yasa tayi saurin fadin." Aa ba nufina kenan ba."

Yace." Idan ba haka kike nufi ba menene na damun kanki?  alamu sun nuna akwai wani abu da yake zuciyarki game da ita Amaryar tawa, kin gane ko bana so ki fito da kishinki tun yanzu yin hakan zai janyo mana samun sa'bani  dake, bana son tashin hankali a gidana kiyi kokarin ganin kin kiyaye faruwar wata matsala."

A sanyaye ta bashi hakuri da fadin" Zata kiyaye insha Allah, zuciyarsa babu dadi yayi mata sallama ya kashe wayarsa ya koma cikin mutane domin cigaba da abunda yake gabansa.

*****

A can masarautar kuwa komai yana tafiya kan tsari wata hatsaniya bata 'kara tashi  ba, sosai Ta samu daidaito da  zaman lafiya da 'yan uwanta, kowa yana kokarin faranta mata rai,   kuma Komai na bukatar rayuwa an tanadar mata har da bayi wanda za taje   dasu gidan mijin nata domin su bauta mata   maza biyu mata biyu.

'Bangaran gyaran jiki kuwa har gajiya tayi domin kullum da kalar maganin da zata  sha, al'amarin da ya janyo mata mugun ciwon mara  wanda take kwana dashi ta tashi dashi ga wani ruwa da take zubarwa wanda ta riga ta fahimci ko na menene,   haka nan take hakuri domin samun farin cikin mahaifiyarta tasan idan ta bijire to za'a ji kansu abunda bata fata kenan babban burinta ta samu ta rabu da ita lafiya.

Ya kasance yau saura sati daya daurin auran Sakina tazo gidan suka rufe kofa suna tattauna maganar,  tace." Kawata ni kuwa zan so ganin wannan mutumin da ya samu wannan gara'basa shiyasa fa mutum in yana da dama a hannunsa ya dama tun  kafin    wankin hula ya kaishi ga dare, don Allah dube ki sankaceciya son kowa kin wanda ya rasa baki da kirar Allah wadai kin tara duk wani abu da ake bukata wanda ya kamata a ce kin kasance matar daya daga cikin shuwagabbanin kasa amma zaki kare a auran wani dan kauye bagidaje mafarauci wanda yake ci a karkashin gwamnati wallahi wannan al'amarin sam beyi min dadi ba."

Ido cike da 'kwallah tace." Ya zanyi Sakina dole nayi hakuri nayi biyyaya  na zauna da mutumin nan domin hakan shine kwanciyar hankalina wallahi nasan idan  na  bijire wa wannan al'amarin iyayena suna iya tsine min  albarka, Sakina baki ga yanda suke 'kaunarsa ba, haka mutumin yake da masifar kwarjini da shiga zuciyar duk wanda mu'amula ta had'asu........Kai tsaye ni ba zan kushe hallitarsa ba domin kyakykwa ne sosai gashi da kirar maza bashi da makusa fa,

domin duk wani abu da mace take nema a gurin namiji ya mallaka hausawa suka juma'ar da za tayi kyau tun daga labara ake ganeta, kin ga dai ban san zahirin sa ba  amma jarumtarsa ke nuna min cewa shi din ba rago bane zai iya daukewa mace dukkanin bukatarta, amma hakan besa naji ina sonshi ba, dalili shi ba abokin burmi na bane, naso an kyaleni na za'bi daidai dani na aura amma shi kaf family nasa mutanan k'auye ne matalauta, shima din akwai gidadanci da 'kauyanci a tare dashi  wannan dalilin da yasa na tsaneshi!  nake jin kunya a danganta shi dani a matsayin mijina, bayan haka bashi da wata makusa a suffar sa."

Tsaki taja da fadin." Wallahi kin bani  haushi sai maganar suffa kike suffarsa ta banza da wofi, me za kiyi da suffarsa  ai yanzu ba'a duba wannan, gabadaya mata sun gane sunyi wayo yanzu basa yarda su kai kansu gidan wahala, ni nan da ki gan ni ba zan ta'ba yarda na auri talaka ba wallahi mai kudin gaske zan aura koda kuwa ya kasance tsoho tukuf babu ruwana da tsufansa kudinsa nake bukata ya fadi ya mutu na samu rabona, idan kuma bukatar namiji ta kamani na fita na samu wanda zai biya min bukata, abunda duk gasu nan mazan da kudi ko babu zasu gamsar dake  amma duk kin damu mutane da maganar suffa da kyau, nan gaba kadan ina kyautata zaton kyawunsa ne zai rinjayeki ."

Girgiza kai tayi da fadin." Baki fahimci magana ta bane shiyasa kike ganin kamar nan gaba zai iya jan ra'ayi na, kawai dai ina fada miki abinda yake zuciyata ne."

Tabe baki tayi da fadin" Ke nifa ban yarda ma dake ba wallahi anya kuwa babu soyayya ba'kauyen nan a cikin zuciyarki, ni dai nasan mutumin da kake qi ba zaka zauna kana kwarzanta shi ba."

Cikin takaici da jin haushin maganarta tace." Sakina mu bar maganar nan haka kada ki 'bata min rai, tunda  dai kin  kasa fahimtata shikkenan bana so mu rabu da bacin ran juna."

'Yar dariya tayi da fadin." Kada kiyi fushi k'awata tsokanarki nake yi amma don Allah bari nai miki wata tambaya."

Ba tare da tace komai ba ta zuba mata ido tana sauraranta.

Tace." Shin wanda za'a aura miki  din mutumin wane gari   ne."?

Jim tayi tana tunani kafin tace."Mutumin Katsina ne cikin wani karamin kauye dake karamar hukumar malunfashi, duk wani binkice daya cancanta Maimartaba yayi akansa da iyayenshi basu da wani aibu kaf family nasu mutanan kirki ne, sai talauci da yayi musu katutu! kaf d'insu matalauta ne asalin sana'ar  mahaifin shi korar jakai,  yanda Maimartaba yake fada mana shi kansa Umar din be taso da mahaifiyarsa ba sai kakarsa wannan shine abinda na sani.

Tace."Okay yanzu dai idan na fahimta can k'auyen zai kai ki ya ajiye."?

Girgiza kai tayi da fadin." Aa na fada miki yanzu yana aiki a karkashin gomnati a matsayin jami'in tsaro, ya samu daukaka sosai dalilin jarumtarsa wannan dalilin yasa gomnatin mallaka masa gida tare da abubuwan more rayuwa yana nan tare da kakarsa a gidan.

Murmushi tayi da fadin." Akwai hanyoyi masu sauki da za kiyi amfani dasu ki cuzgunawa rayuwarsa, ki hana shi jin dadi, sannan ki hana shi zaman lafiya, ni zan zan baki shawarwari masu kyau yanda za kiyi ki ha nashi kwanciyar hankali dashi da kakar tasa."
Ajiyar zuciya ta sauke cikin jin sasauci tace." Nagode sosai k'awata.

A daran ranar ta sake kiran wayarsa tun bayan kiran da tayi masa ya d'ankara mata magana mai zafi, to wannan karon a shirye take dashi tayi alkawari kan cewa duk cin mutuncin da yayi mata sai ta rama.

Koda yaga kiran nata beyi kasa a gwiwa ba ya amsa cikin muryarsa mai cike da amo!!

Ji tayi ta daburce sakamakon jin sautin maganarsa a kunnuwanta, da sauri ta aro jarumta kafin ta fara magana cikin Izzah! da isa! tace." Kana jina dai ko."?

Ya maimaita maganar a fili da mamakin yanda take masa maganar gatsar kamar uwarsa.

Be tanka mata ba kuma be kashe wayar ba.

Ta sauke zazzafar ajiyar zuciya wacce taso ta jefe shi cikin wani yanayi yayi saurin janye wayar daga kunnashi, sai da ya daidaita nutsuwarsa sannan ya mayar da wayar kunnanshi da fadin." Ke nake sauraro."

'Karamin tsaki taja za ta cigaba da magana ya katseta da fadin." Na tsani wannan da'bi'ar taki ke kuma na fahimci abinda kika sa a gaba kenan rashin d'a'a da tarbiya, ayi miki magana kiyi tsaki! to kada ki kuskura kizo gidana da wannan da'biar zaki sha wahala a hannuna."

Wani kuttun takaici yazo ya tsaya mata a wuya! wai gargadinta yake kamar wanda aka gaya masa cewa tana san zama dashi al'amarin ya bata mamaki mutu'ka ta daure ta had'iye bacin ran kafin tace." Magana nake so nayi da kai ni bakar magana nace ka gaya min ba saboda haka ina so ka tsaya ka saurareni."

Ya kalli agogon dake kafe a dakin goma saura na dare dawowarsa kenan ya kwa'be kaya zai shiga wanka ta kira shi, yace." Ni nafi ki Uzuri wanka zanyi yanzu naci abinci na kwanta domin yau gabadaya a tsaye na yini ina bukatar hutu a halin yanzu saboda haka minti uku na baki kiyi sauri ki fadi abinda ke tafe dake ina sauraranki.

Wata 'kwalla mai zafi ta ciko idonta, wai shin za tayi da wannan mutumin ne, wato bama shi da cikkken lokacin da zai saurareta.

Hanci taja kamar ta fashe da kuka saboda tsabar bakin ciki da takaici tace." Matsalar kace wannan, abinda nakeso na fada maka shine ni ba zan zauna gida d'aya da kowa ba, idan wannan ne tunaninka sai ka sauya wani."

Ya jima yana jajanta maganar a cikin zuciyarsa kafin yace." A yanzu dai baki isa ki tsara min yanda zanyi ba, ballanatana kuma kina k'arkashi iko na, kafin na san kowa a duniya Uwale na sani, saboda haka akan ki dai ba zan rabu da ita ba Ina tare da ita, duk inda nasa 'kafa zata ajiye tata, Idan kuma kina ganin zaki zo da gurin zama daga gidanku to ni zan baki fili ki dasa ki zauna ke kad'ai, amma ni ina tare da Uwale muddun rai insha Allah."

Tace." Kana maganar nazo da gurin zama ai kasan nafi 'karfin wannan, kai ne matalauci ba'kon arziki da har kake wani tutiya! da arzikin gomnati, to shikkenan tunda kana ganin ba za kayi abinda nace ba, to kuwa kullum kana tare da bacin rai a cikin gidanka."
Bata jira jin ta bakinsa ba tayi saurin kashe wayar tana wani irin numfarfashi irin na b'acin rai!

*Kika futar min da littafi keda Allah! ki ka karanta baki biya ba kema keda Allah!*

*#500via.....0542382124.....Binta umar gtbabk, idan kati zaki turo kiyi min magana ta WhatsApp da wannan number.... 07084653262.....BINTA UMAR ABBALE*
[1/30, 6:24 PM] Matar Malam: *GJSR*
*47&48*
Cikin tsantsar 'bacin rai da damuwa ya samu gefen gado ya zauna yana auna maganganunta, "Kai ne mataulaci ba'kon arziki wanda yake tutiya da arzikin gomnati to tunda ba zaka yi abunda nace ba kullum zaka kasance cikin bacin rai." Wa'innan maganganun sune kawai suke masa amsa kuwwa a kunne! babu shakkah auran wannan yarinyar bashi da fa'idah a gurinsa, Dole abunda yake gudu babu makawa sai ya faru, tun kafin ta shigo gidansa ga irin furucin da take a kansa da famliy nasa, Annabi SAW yace ku auri salihan mata masu hankali da tarbiya duk wanda yake so ya gina zamantakewar auransa dole ya cire son zuciya gami da rudin duniya ya nemi nagarta ya aura, yarinyar ta tara komai na hallita wanda zata iya ja ra'ayinsa amma ta samu nakusu gurin mugun hali da rashin tarbiya, tana ta'kama da kudi da mulki da suffar jiki, wannan dalilin yasa take ganin tafi karfin kowa babu wanda ya isa ya tursasata! dama haka

rayuwa take, ya jima yana addua akan Allah ya arzurta shi da mace tagari dalilin tsoro da gujewa hallayarsu, hakan yasa be tsawwalawa rayuwarsa akansu ba duk da cewa yana da bukatarsu amma bai bari hakan yayi tasiri a zuciyarsa da gangar jikinsa ba, ya cigaba dai da addua da neman zabin Allah, sai gashi kuma Allah ya jarabceshi da auran yarinyar da kwata-kwata tunaninsa be kai kanta ba, hakika kowane bawa yana tare da jarrabawarsa..................babu shakka shigowar yarinyar rayuwarsa babban kalubane a rayuwarsa tunda ya fahimci cewa shaid'aniya ce bata k'aunar zaman lafiya da kwanciyarsa hankali, dole ya zage damtse a kanta ya nuna mata bambancin mace da namiji, babu ruwansa da mulki da sarautarta domin basu ne a gabansa ba, mutukar an d'aura auran nan to dole ta zauna karkashin ikonsa ko tana so ko bata so kuma ba zai yarda da shirme da shashanci ba, kullum maganarta bakin rijiya ba gurin wasan makaho bane to shine zai tabbatar mata da hakan daga zarar ta shigo gidansa zai nuna mata cewa ita ba komai bace a gurinsa.

Da wannan tunanin ya shiga wankan yana sake jin tsanarta a cikin zuciyarsa duk wasu iskanci da take masa bai ta'ba jin haushinta irin yau ba, in banda hauka da jahilci waye yayi mai kudi da talaka idan ba Allah ba, maganar yana ci da gomnati ai halak yake ci ba sata yayi ba, to duk wannan ma bai dameshi ba sosai akan yanda take kokarin kafa masa dokoki wannan shine yafi 'bata masa rai! yana samun nutsuwa zai auri wacce zata kwantar masa da hankali yayi rayuwar jin dadi da ita wannan shine shawarar da ya yanke.

*****

A cikin 'yan kwanakin da suka rage a daura auran gabadaya ta sauya tayi wani bal'in kayau na mussaman fatar ta tamkar kasa harshe ka lashe domin kyau da taushi sai sheki take saboda gyara na mussaman da Mamanta tasa ake mata, in ta zauna a guri kuwa har ta tashi kamshinta yana gurin, tasha gyara ciki da waje, wanda yake janyo mata feelings sa'i da lokaci shiyasa wani lokacin take fakar ido ta zubar da rabin maganin a toilet domin ita kadai ta san halin da take shiga idan sha'awarta tashi,

Sosai ta jinjinawa mamanta ta kuma yaba da kokarinta a kanta, sai dai kash duk wannan gyaran da ake har yanxu zuciyarta ta nan a kangare bata jin za taje gidan mijin nata da sigar san zaman lafiya.

Asp ya kira wayarta suka gaisa a mutunce da yake yanzu ta saki jiki dashi dalilin matarsa aunty Zeey kenan, suka dan ta'ba hira kafin ya shiga tsokanarta da fadin" Yau saura kwana biyu ki zama amaryarmu ina fatan dai yanzu kun sansanta da mutumin naki."?

'Bata fuska tayi tace." Asp ka daina yi min maganar wannan mara kirkin abokin naka saboda ya same ni a arha shine har ya samu damar kira na da *Matar ladan noma* to ka fada masa cewa koda na shigo gidansa yayi kokarin samun zaman lafiya dani, idan ba haka ba wallahi sai na hana shi kwanciyar hankali domin auranshi kaddara ne a tare dani, domin ni nafi karfinsa ni ba

matar k'ananun yara bace."

Maganganunta sun bashi haushi da dariya amma bai yarda yayi dariyar ba ya danne cikin taushin murya yace." ZINATU wai me yasa ki ke haka ne? me kika dauki duniya? ita fa mace duk isa da kasaitarta gidan mijinta shine mutuncinta, duk da bakya san abokina amma bai cancanci haka daga gurinki ba, na tabbata cewa kece kika tunzurashi har ya kira ki da wannan kalmar *Matar ladan noma* wanda ni kaina nasan ya fad'a ne domin ya 'bata miki rai amma matan da za'a kira da irin wannan sunan kwata-kwata bakya cikinsu, ina mai tabbatar miki da cewa abokina yana sonki, abunda yasa ki ka kasa gane kansa wannan dabi'un naki marasa kyau! shi mutum ne wanda baya son raini ko kadan, yana da zafi! shiyasa bana so kije gidansa da wannan dabi'un naki, don Allah kiyi hakuri ki dauka cewa auransa alkairi ne ki zauna lafiya dashi da 'yan uwansa."

Baki ta ta'be da fadin." Asp ni ba zan yarda da wannan maganganun naka ba, kawai kana so ka tsara ni ne idan ba haka ba yaushe zaka zo kana fada min cewa yana sona ai da yana sona ba zai so bacin rai na ba, sannan duk abunda nace ina so sai yayi min amma tsakanina dashi kullum ba'kar magana kafada masa cewa a shirye nake idan ya bukaci ya zauna lafiya dani kansa, idan kuma tashin hankali yake bukata ashirye nake."

Da sauri ya tare ta da fadin." Mugun ji da mugun gani Allah ya tsare mu, bama neman tashin hankali kullum alkairi muke nema ZINAT Abokina zuma ne (ga zaki ga harbi) duk da ban dade tare dashi ba amma na karanci halayyansa tsaf, yana da saukin kai ga wanda ya fahimceshi baya san tashin hankali zaku jima wani sa'bani bai shiga tsakaninku ba, mutukar ka kiyaye abunda zai kawo muku samun sab'anin, ina so ki rike wannan don Allah na ro'ke ki, ki zauna lafiya dashi kada ki bari shaid'an ya samu nasara a kanki.

Murmushin takaici tayi kafin tace." Ranka ya dad'e na rasa me yasa kake tsoron wannan abokin naka kullum kai kenan gurin yi masa campaign kana kare shi to ni duk abunda zaka fada a kansa ba zai sanya naji tsoronsa ba, ka fada masa cewa nafi karfin wannan b'akin kwallin da yake rambad'awa a idanuwansa, kuma be isa ya firgitani ba."

Dariya yayi kafin ya girgiza kai da fadin." Kinga mu bar wannan maganar tunda kin kasa fahintata, yanzu wane shirye-shirye kike yi game da hidimar biki."?

Baki ta ta'be ta yatsine fuska da fadin." Wane irin shirye-shirye sai kace wacce za tayi auran so, ni babu wani shiri da nake kuma bana bukatar komai daga gurinku.

Yace." A haba dai gimbiya koda ba auran so bane yana da kyau ki d'an yi gyare-gyare domin ki fita daban a cikin mutane kasancewarki amarya, wannan hakkinki ne, ki fadi ko nawa kike bukata sai na tura miki yanzu."

Dariyar takaici tayi kafin tace." Ranka ya dade na fada maka fa duk campaign din da za kayi masa wallahi baku isa ku sayi soyyayata ba, ka fada masa cewa har yanzu bai kai wannan matsayin ba,har yaushe yayi arzikin da zai zo yayi wa mutane tutiya dashi."

Asp ransa ya b'aci  da jin maganarta, Yace." Wai ke mai yasa kike hakane? ina yi miki kallon mai ilimi amma kina aikata aiki irin na jahilai,  Zinatu girman kai da izzah duk ba dabi'u ne marasa  kyau! don Allah ki daina sannan ki daina daukar kanki daban da mutane dukkaninmu Allah ne ya hallice mu, shine kuma yayi mai kudi da talaka kuma shi yake bada mulki ga wanda yaso ya kuma hana wanda yaso, kada kiyi mamaki Allah zai iya musayan miki rayuwa, ki zama mak'askanciya wannan kadan kenan daga irin hukuncinsa, ki gane duniya dan Allah."

Shuru tayi da alama nasiharsa ta shige ta.

Ya sauke numfashi da fadin." Kin san Allah duk wannan kai da kawon  da na  keyi  akan wannan al'amari UMARU be sani ba, amma magana kadan sai kice ina masa campaign  ai ba sai munyi campaign ba tunda an riga an bamu kyauta  wane campaign za muyi." Cikin zolaya ya 'karashe maganar.

Ta  kuwa fusata! da fadin." Ina ganin mutuncinka fa kada ka 'kara yi min irin wannan wasan."

Ya tsagaita dariyar da yake da fadin." Na daina ranki ya dade yanzu ake hukuma ce sai da rarrashi duk  da an bamu kyauta muna godiya domin  mun san ba karan mu ne ya kai tsaiko ba, dami a kala muka tsinta."

Ya mutse fuska tayi da fadin." Shikkenan ni zan kashe wayar sai an jima."

Yace." Ai bamu gama ba.

A k'agauce tace." Saura me kuma Asp idan kun kwantar da hankalinku saura 'yan kwana ki aka kawo muku ni." Yace." Ni da kaina ma zanzo na dauke ki tunda kin san mutumin naki baya gari yana gurin training ni ya bar wa wuka da nama."

Shuru tayi ba tace uffan ba.

Yace."Yanzu nawa kike bukata."? babu wasa yayi maganar.

Itama cikin rashin wasa tace." Bana bukatar ko kwabon ku."

Murmushi yay da fadin."Shikkenan tunda kin ce haka mu dai mun fita  hakki dan kada watarana ayi mana gori."

Cikin takaicinsa tace." Sai an jima kace ina gaishe da da k'awata."

Ba ta jira jin abinda zai ce ba ta kashe wayarta tana jan tsaki, gabadayansu haushinsu takeji, magana d'aya da yayi itace ta tsaya mata a rai..........Inda yake cewa duk wannan abubuwan da yake abokin nasa bai sani ba, ita ai ta dauka shine ya wakiltashi kafin yayi tafiyar yazo ya kafa masa gwamnati a gurinta, tsaki mai tsayi taja kafin ta nufi toilet da bacin ran hakan a cikin ranta.

Cikin baccin da ya fara daukarsa yaji alamun kira ya shigo wayarsa.

Hannu yasa yana laluban drowar da wayar ke kai.

Murmushi yay ganin mutumin shi ke kira.

Yasa wayar a kunnashi tare da sallama a bakinshi.

Daga daya bangaran Asp din ya amsa da fadin." Jarumi ya na jika wani iri ne ina fata dai lafiya."?

Ya bude murya sosai da fadin." Lafiya lou wallahi bacci ne ya fara daukana kiran wayarka ya tashe ni."

Yace."Okey yau kun dan samu hutu kenan."

Hamma! yayi kafin yace." Eh amma hutun duka na two hours shine dalilin da yasa na kwanta domin na rage baccin dake idona.

Yace."Hakan yana da kyau mutumina, shin kana waya mutuniyar kuwa."?

Murmushi yay wanda ya tsaya iyakar fatar bakinsa ya fahimci wacce yake nufi shiyasa yayi murmushin takaici.

Asp yace." Tunda naji wannan murmshin naka na san baka d'auki shawarata ba, UMARU na fada maka fa dole a wannan ga'bar kai ka sauka kabi yarinyar a sannu a hankali kafin ta shigo gidanka, idan ta shigo shine zaka nuna mata kai ne a sama da ita, har yanzu ka kasa gane hallayar 'ya'ya mata, wallahi da ka dauki shawarata da tuntuni yarinyar nan ta bada kai bori ya hau, na fada maka tana bukatar rarrashi da nuna kulawa mybe *Ilove you* wannan ka kasa fad'a mata wanda ni nayi imanin da cewa abinda take bukata kenan."

Ajiyar zuciya ya sauke da fadin." Asp wannan yarinyar fa bahaguwace! kai ne har yanzu baka fahimta ba kake ganin nuna kulawa ko kuma *I love you* zasu sanya ta daina rashin mutunc! a

haka take, haka Allah ya halliceta zan iya karyar mata da kaina domin samun soyayyarta ta dizgani girmana ya zube a banza a wofi, ni bana wahalar da kaina a in da na san ba zan samu biyan bukata ba.

Yace." Kai ne dai kake ganin haka, amma ni nayi imanin cewa kabi wannan matakin wallahi sai ka sameta a hannu kuma ka gwada ka gani."

'Yar dariya yay da fadin." To shikkenan zanyi kokarin ganin nayi abinda kace duk yanda mukayi da ita za kaji."

Yace."Yawwa haka nake so na ji  yanzu nima muka gama waya da ita na kira ta domin jin abunda take bukata na hidimar biki, tace bata bukatar komai daga gurinku kuma tace lallai na sheda maka cewa duk  irin campaign din daka turo ni gurinta to ba zaka samu abunda kake so ba.

Dariya ya fashe da ita, ya dinga yi yana girgiza kai ya ma kasa magana saboda yanda dariyar taci karfinsa.

Asp shima yana dariyar yace." Ai ban ta'ba ganin rigimmiyar yarinya irin wannan ba, amma na fahimci nasiha tana ratsa ta wannan ma makami ne wanda ya cancanta ka rike hannu bibbiyu.

Dakatar da dariyar yayi da fadin." Asp maganar nan ta bani dariya da haushi wallahi  amma dai dariyar tafi yawa,  lokacin da tace maka kana yi min campaign sai kace mata kai din ubangidana ne kafi karfin kayi min fadanci ko wani aiki, amma na san da wuya ka iya mayar mata da martani.

Yace."Ni da nake kokarin ganin an raya sunnah ma'aiki SAW  yaushe zan dagula al'amarin ai duk abunda tace  dai-dai ne, amma ina kokarin ganin na nusar da ita idan tayi wani shirman."

Yace." Nagode sosai abokina, yanzu a wace matsaya kuka tsaya."?

Yace."  Tunda tace bata bukatar komai namu shikkenan, amma na fada mata cewa kada daga baya tazo da wata magana.

Yace."  Kwarai kuwa tunda an fita hakkinta wannan shine sharadi."

Yace." To kaji yanda mu kayi da ita insha Allahu kuma za'a gabatar da komai cikin tsari amma ya kake gani? shin a ranar da aka daura auran za'a daukota ko kuma sai washe garin ranar."?

'Dan 'bata fuska yayi da fadin.'' Aa ana d'aurawa ka d'auko ta, bana tsammanin ma mahaifinta

zai bari ta sake kwana a gidan mutukar an d'aura auran."

Yace." Okey to shikkenan hakan dama shine tsari mai kyau, insha Allah zanyi kokarin hakan ya tabbata."

Yace." Godiya nake abokina Allah ya kara zumunci ya kuma bar abotar mu." Ya amsa da "Amen ya rabb mutumina ka wuce aboki a gurina a matsayin dan uwa kake a gurina."
Cikin wani irin farin ciki yace." Haka kake a gurina wallahi jinka nake tamkar wanda muka fito ciki d'aya Allah ya kawar da idon makiya a tsakanimu." Ya amsa da "Ameen ya Allah, kafin suyi sallama da juna.

*****

To a daran ranar da sukayi wannan tattaunawar da Asp din ya yanke wata shawara wacce yake ganin zata taimaka masa gurin tantance nagarta da kamun kan yarinyar........ da yake yana amfani da layin waya biyu sai yayi amfani da d'aya layin da ba kowa ya san shi dashi ba, wata irin rikitacciyar wasika ya tura mata mai dauke da zafafan kalaman soyayya da tsuma zuciya, sosai yayi amfani da hikima gurin shirya kalaman wanda yake da tabbacin cewa dole su rikirkita mata lissafi, bai fayyace mata kansa ba asali ma babu suna a wasikar yana tura mata ta in box ya cire sim card din ajiyeshi cikin cover shi sai an kwana biyu zai mayar.

Kamar yanda yayi tsammani hakan ne ya faru, domin tunda ta karanta wannan text din gabadaya ta rikice ta rasa abinda yake mata dad'i a duniya, macace mai bala'in son soyayya da kulawa shiyasa kullum cikin kallon indian film take amma irin na soyayya, tana bala'in san wanda kullum zai dinga kasheta da kalamai yana rarrashinta ita kuma tana masa shagwaba da sangarta irin yanda take so, kasa hakuri tayi tabi layin da kira, sai dai ta kisa sau goma ana ce mata layin baya aiki a halin yanzu, hawaye masu zafi ta share tana tunanin daga wace duniya sakon wasikar yazo gareta? wanene wannan wanda yake da kalamai irin haka? shin a ina ma ya samu number ta, hakika zata so ganin sa ido duk talaucinsa zata iya zama dashi mutukar zai dinga lallabata yana bata abincin zuciya irin wanda take bukata.

Hanci taja tasa hannu ta goge hawayen dake karakaina a saman fuskarta, me za tayi da wancan ba 'kauyen mutumin da be iya komai ba sai 'bakar maganar magana, tunda take dashi bai ta'ba yi mata kalami mai dadi ba, ko a lokacin zaman su a daji ta lura kan dole yake rarrashinta idan wata masiba ta sameta, a halin yanzu ya kamata ace ya kwantar mata da hankali domin samun soyayyarta amma saboda girman kai ya kasa duk sanda zaiyi mata magana cikin gadara! da isa! shi ba kowa ba sai iko yake nuna mata ita kam ba zata yarda da wannan ba, tunda dai a zahiri tana ganin ta fishi da komai ba zata yarda ya mulke ta ba har yanzu tana nan akan bakanta ko auran sukayi.

Kullum sai ta gwada kiran layin sai ace mata baya aiki, duk ta susuce! tunaninta ya kammanin mutumin yake? ba abunda take so taji sai muryarsa.

A na gobe daurin auran da daddare kowa yai bacci ta gwada kiran layin, jin yana shiga yasa ta tashi zaune da saurin gaske farin ciki gabadaya ya cika mata zuciya burinta kawai ya daga wayar taji sautin muryarsa.....

*Kika futar min da littafi keda Allah! ki ka karanta baki biya kema keda Allah!*

*#500via.....0542382124.....Binta umar gtbabk, idan kati zaki turo kiyi min magana ta WhatsApp da wannan number.... 07084653262.....BINTA UMAR ABBALE*
[1/31, 9:53 PM] Matar Malam: *49&50*
Cikin wata murya mai sanyi da ita kanta bata san tana da ita ba tayi sallama kafin ta dan lumshe idonta tare da sauke ajiyar zuciya tace." ina so na san da wanda nake magana a halin yanzu."

Shuru yayi bece uffan ba, gabad'aya mamaki ya gama kashe shi jin irin salon da take masa magana ashe ta iya tausa murya haka.

Shuru be ce mata komai sai saukar numfashinsa da takeji a kunnawanta.

sai gabadaya jikinta ya sake rikicewa, haka kawai Allah ya jarabce da son wanda bata ta'ba gani ba.

Cikin 'yar shagwaba tace." Please don Allah waye ne? kwana biyu da suka wuce naga text dinka shine dalilin da yasa ma na kira ka domin san kowaye kai ."

Idonsa a lumshe yayi d'an gyaran murya kamar zai yi magana sai kuma yaja bakinsa yay shuru, gabadaya ta gama kashe masa jiki da salon da take masa magana yana masifar son shagwabbiyar mace.

Jin yayi shuru ta sake narkar da murya dan a zahiri saura kadan ta fashe da kuka tace." Ba za kayi min magana ba ko? ka san kuwa halin da ka jefa zuciyata."?

Zaune ya tashi yana sake rike wayar a kunnunsa, kafin ya aro wata murya da duk bin diddigin mutum ba zai gane muryarsa bace yace." Wani bawan Allah ne yazo da kokan baran shi a k'urataccan lokaci."

Jikinta ya 'kara saki jin sanyayyiyar muryarsa ya jefa ta cikin wani yanayi mai wuyar fassaruwa, tace." Kayi min bayanin kanka daga ina kake kuma ina ka samu number ta."?

Dan murmushi yay kafin yace." Sunana FARUK ni dan asalin hajar katsina ne." Gabanta yay fadi jin ya ambaci garinsu ma'kiyinta.

Jin tayi shuru ba tace komai ba ya cigaba da cewa."  Na tsinci hotonki a social media gurin wani biki sai kawai Allah ya jarabceni da tsananin sonki da kaunarki,  talaka ne ni amma ina da zuciyar nema,  duk da na san cewa ke ba tsaran aure na bace,   hakan bai sa na saduda ba sai da nayi fafutukar samun number ki,  amma wanda ya bani number ya sheda min cewa aure za kiyi hakan be firgitani ba, tunda dai ba'a daura auran ba zan fito na nuna miki tawa soyayyar da take gudana a cikin jikina."

Tun sanda ya fara maganar take share hawaye, tayi duk yanda za tayi ta tsayar da kukan abun ya fassakara, tana kukan  tace." Kazo a 'kurataccen lokaci bawan Allah, sosai  nake son mai sona kuma ina alfahari da soyayyarka, hakika da kazo a kan ga'bar da iyayena suka yanke min hukunci to babu shakka  kai zan nuna musu a matsayin mijin aure, babu ruwana da talaucinka mutukar zaka bani abincin zuciyata bani da damuwa,  yanzu maganar da nake maka gobe za'a daura min aure da wani wanda bana ra'ayinsa." Cikin  wani irin kuka  mara sauti takarashe maganar.

Jikinsa ne ya mutu jin kukanta yake har tsakiyar kansa,  Cikin taushin murya da sigar rarrashi yace." Yi shuru ki daina kuka kinji ko wannan kukan da ki ke yana ta'ba min zuciyata ina jin kamar nazo inda kike na rarrasheki bana son zubar hawayenki.

Hannu tasa ta goge hawayen  amma ba tace komai ba.

Ajiyar zuciya ya sauke kafin yace." Yanzu ya za kiyi dani da soyayyata Gimbiyata bana jin zan iya rabuwa dake fa.''

A sanyaye tace." Nima bana tunanin hakan a zuciyata, ka bari a kwana biyu zan yanke shawara akan soyayyarmu."

Murmushin takaici yay kafin yace." Okey na fahimta yanzu zamu cigaba da gaisawa ne ta waya babu matsala hakan."?

Shuru tai na minti biyu kafin tace." Babu matsala amma ka bari ni zan dinga kiran ka"

'Yar dariya yay da fadin." Shikkenan my love yanda ki ke so hakan za'ayi amma inaso muna gaisawa koda ta charting ne."

Ba tare da damuwar komai tace."Wannan  babu damuwa zanyi serving number naka yanzu."

Yace."To ina godiya my princess bari na barki ki kwanta ki huta ko, amma ina tabbatar miki da cewa yau ba zan iya rintsawa ba."

Da sauri tace."Saboda me."? Cikin tausayawa kansaYace. " Saboda gobe za'a daura miki aure da wani."

'Karamin tsaki taja kafin tace." Ka kwanta kayi barcin ka, kada kasa damuwar komai a ranka domin wanda za'a daura min aure dashi, bashi da wani muhimmanci a zuciyata, bana sonsa bana ra'ayinsa, da auransa da babu duk daya suke a gurina, ka kwantar da hankalinka nayi maka alkawari kai zaka mallake ni, domin da kai zuciyata ta aminta duk da ban ta'ba ganinka ba ina hasaso fuskarka a idona, ina sonka a duk yanda kake, zanyi mana duk wani kokari da zai tabbatar mana da biyan bukatarmu."

Yaji haushi da takaicin maganarta amma sai ya danne a zahiri ya nuna mata farin cikinsa, sallama yay mata da jin zafin maganganunta a zuciyarsa ya kashe wayar yana tsaki da fadin." Sakarai mara wayo kawai."

Kwanciya yay yana tunaninta, gabadaya ma ya raina wayonta da dubararta, koda yake macace mai rauni zata iya yin abinda yafi haka.

Agogon ya d'an duba, yanzu minti talatin kenan da wayarsu, ya kama sha daya dai-dai na dare, yanzu da Asalin number shi ya kira ta.

Sai da ta kusa katsewa sannan ta dauka tana cin magani, wayar tasa a kunne amma ba tace komai ba.

Yay mata sallama cikin asalin muryarsa mai cike da amo!!

Ciki-ciki ta amsa tana ya mutse fuska.

Yace." Tun dazu nake kiran wayarki sai ace dani busy shin dawa kike waya a cikin wannan daran."?

Cikin tsiwa da gadara irin yanda take masa magana tace." Ina ruwanka da wanda nake waye? ko kana da damuwa da hakan ne."?

Daurewa yay yace." Ni nake da damuwa da hakan kuwa, dalilina kuwa nasan baki nutsuwa da kamun kai zaki iya raba dare da wani namijin a waya saboda rashin kintsi."

Zuciyarta ta dinga wani irin zafi da tukukin bakin ciki!

Abinda yake had'ata dashi kenan bakar magana, kwata-kwata be iya rarrashin mace ba,  haka kawai zai tayar mata da hankali tana zaman zaman ta.

Murya na rawa kamar me shirin fashewa da kuka tace." Bagidaje kawai kana da matsala wallahi, haka kawai zaka shiga rayuwata cikin daran nan to ta Allah bata ka ba"

Yay dariyar cusa takaici yace." Naji bagidajen ne dole kuma a zauna dani a haka na kuma bada umarni ayi ko ana so ko ba'a so."!

Tsaki mai tsayi taja irin wanda ta san baya so tace." Wahalalle kawai bani da lokacinka." Da sauri ta kashe wayarta domin bata so ta sake jin sautin muryarsa!

Bacci k'auracewa idonta yay ta dinga zubar da hawaye tana tunanin boyayyan masoyinta daya bayyana mata kansa a yau..........Shin wai ya za tayi da wannan takad'irin mutumin da ake kokarin aura mata  bayan be tara duk abunda take da bukata ba.

Haka ta kasance cikin tsananin damuwa gami da juye-juye sai gefin asubah bacci mai nauyi ya d'aukata.

Shigar aunty Hassana dakin yayi daidai da bude idonta gari ya waye tarwai.

Zaune ta mike tana dan ya mutse fuska! wani irin ciwo kanta yake ba komai ya janyo mata hakan ba illah kwanan kuka da tunanin da tayi.

A nutse ta 'karasa kusa da ita ta tsira mata ido na minti  biyu kafin tace." Sai yanzu ki ka tashi kenan."?

Kai ta daga a raunane tace." Aunty an d'aura auran ne."?

Girgiza kai tayi da fadin." Sai goma da rabi tukkuna, na shigo ne domin naga ko kin gyara jikinki ashe ke kina ma kwance."

Kai ta dafe da fadin." Jiya ban samu bacci ba sai gefin asubah, shiyasa ban tashi da wuri ba ko sallah fa banyi ba."

Tace." Zinat ba zaki sanyayawa ranki ba ko? me yasa kike so ki jefe kanki cikin wani hali, iyayenki fa ba zasu ta'ba cutarki ba."

Tace."Aunt Hassana don Allah mu bar wannan maganar domin ni ba wannan  ne dalilin  ya hana ni  bacci ba, ai na hakura na barwa Allah."

Tace."Okey to  idan hakane ki tashi ki gyara jikinki kiyi kwalliya sosai tunda kinqi yarda da ayi

miki kitso da kunshi (lalle) irin na amare  kada dai  ki yarda  mu da muke 'yan gayya mu fiki kyau zakiji kunya.

Murmushin takaici tayi tana kokarin saukowa daga gadon tace." Bana ra'ayi ne kawai, amma ban ha naku kuyi kwalliyarki ku ba, ban damu ba idan kun fini kyau."

Hanyar toilet ta nufa jikinta duk a sanyaye........Aunty Hassanar ta bita da kallo tana girgiza kanta, ta rasa wane irin hali ne da ita gabadaya a baud'e take.

Wani dan'kareran les ta fito mata dashi kudinsa ya kai dubu dari da wani abu  rigar bubu ne anyi ado da wani irin net bayan stones din dake jikin les din an kuma baza wani stones din masu walwali a jiki,  c-green ne,  color shi tayi kyau sosai.

Duk wani abu da ta san za tayi amfani dashi sai da ta fito mata dashi ta ajiye mata.

Tana kokarin fita daga dakin, kira waya ya katse mata hanzari.

Ta dawo ta dauki wayar tana dubawa, sunan ba'kauye ne yake yawo kan fuskar wayar.

Cike da mamaki take duba wayar, waye wannan kuma? toilet din ta kalla, ta san halinta tun tana yarinya take da nawa bata da zafin nama haka take idan ta shiga wanka sai an manta da ita.

Yanke shawarar daga wayar tayi a nutse tai sallama.

Jin sabuwar murya cikin nutsuwa yasa shima ya amsa a nutse da fadin." UMARU ne."

Da sauri tace." Angon ne ashe kayi hakuri tana bandaki sai dai idan ta fito ko."

Yace."Babu damuwa idan ba matsala ina so na san da wa nake magana."

Murmushi tai kafin tace."Hassana ce  yayar amaryar taka.

Yai murmushi da fadin." Ai kinga tambayar tayi amfani Auntynmu ya hidima da jama'a."?

Tace."Alhamdulillhi wallahi, Allah dai ya sanya alkairi ya baku zaman lafiya UMARU kayi hakuri da yarinyar nan daban take a cikinmu tana da wani irin hali, amma kuma idan ka'iya zama da ita tana da sauki kai da iya mu'amula."

Yace." Kada ki damu aunty insha Allah zan rike amanarku zan iyakar bakin kokarina."

Tace." To mungode sosai Allah ya baku zaman lafiya."

Ya amsa da ameen ya Allah ya dora da fadin "bari na bari zuwa an jima zan sake kira."

Tace."To shikkenan babu damuwa." Sallama sukayi  ta zauna zaman jiran fitowarta.

Ido suka hada lokacin data fito daga toliet din tace."Wai dama kina zaune har yanzu."

Tace."Nazo fita ba k'auye ya kira wayarki."

Saurin kallonta tayi  suka hada ido ta girgiza kanta rai a bace tace." Kin ji kunya ko."?

Girgiza kai tayi tana dan tabe baki tace."Wane irin kunya kuma." Gaban dressing mirror ta wuce tana ya mutse fuskarta.

Aunty Hassanar tace."Kullum kina nuna mana cewa kin saduda ashe ba haka bane, a zuciyarki don iskanci ki rasa da wane suna za kiyi serving number sa sai da ba k'auye wai shin ma dame ki ka fishi kin san dai baki fishi kyau ba."

Tana 'yar dariya tace."Aunty Hassana ai sunan da ya dace dashi kenan, d'an k'auye ne dashi da family sa,  kinga kuwa babu laifi don an kira shi da wannan sunan  ba kauye bagidaje."

Ta girgiza kai cikin takaici  tace." ki cire wannan sunan bai dace ba, gwara  kisa masa sunansa na Asali hakan shi yafi mutunci."

Saboda bata san suyi ta ja'in ja   yasa tace."To shikkenan aunty zanyi yanda ki kace din, amma da ya kira me yace miki."?

Tana kokarin mikewa tace." Be ce komai ba zai dai sake kiran ki abinda fada kenan.

Ta'be baki tai ta cigaba da shafa mai a fatar jikinta.

Aunty Hassanar tana kokarin fita daga dakin ta dakatar da ita da fadin." Aunty Hassana ya maganar mutanan da aka tura su shirya min daki."

Tace."Ai babu wannan maganar domin mijin naki ya shedawa Maimartaba cewa ke kadai yake bukata akwai komai na bukata a gurin da zaki zauna wannan dalilin yasa aka rushe wacan maganar.

Ta girgiza kai da fadin." Wannan ai zubar da kima da mutunci ne, Aunty Hassana cikinku wa aka ta'ba yiwa haka? ai na dauka kowacce sai da aka cika mata daki uku da kaya amma ni saboda ba'a sona za bar ni haka, to wallahi  babu wanda ya isa na dogara dashi da kayansa.

Hannu ta daga mata da fadin." Wannan maganar Maimartaba zaki samu ki fada masa bani da kika raina ba, Zinatu kije ki samu mahaifinki ki nuna masa cewa baki yarda da hukuncinsa ba, wannan shine zai tabbatar mana da cewa kin fita zakkah a cikinmu."

Tana gama maganar ta bude dakin ta fita ranta a mugun 'bace! addua ce kawai zata shiryar musu da ita.

Hawaye masu zafi suka dina sauka a saman fuskarta, wannan tozarci dame yay kama? kamar ita 'yar gata gaba da baya amma a kaita gidan aure babu kaya sai kayan miji wanda ta raina bata daukashi a bakin komai ba, kwata-kwata ba'ayi mata adalci ba.

Kiran wayarsa ne ya katse tunaninta, da sauri ta dauki wayar tasa a kunne sai ajiyar zuciya ta saukewa cikin kuka tace." Bana bukatar komai naka a gurin da zan zauna, ka kwashe komatsanka zanzo da nawa baka isa na dogara da kai da abunka ba."

Tun wayewar gari ya tsinci kansa cikin walwala da farin ciki, wanda shi kansa ya kasa gane dalilin............Wannan shine dalilin yasa maganganunta ba suyi masa zafi ba, yay murmushi irin wanda ya saba kafin yace." To ke meye na damuwa bayan baki da niyyar zaman auran, ai zuwa da kayan daki zai miki wahala shiyasa na hutashsheki, bayan haka kuma nima haka na samu gidan cike da kayan more rayuwa gwamnati ta zuba min, kada ki damu sashenki daban sai kin so zaki ga wani kuma baki da matsalar komai, wannan dalilin yasa na shedawa Maimartaba cewa ke kadai nake da bukata."

hanci taja kamar za tayi magana sai kuma taja bakinta ta tsuke kokarin kashe wayar take yayi saurin fadin." 'Karfe nawa ma za'a daura auran."?

A kufule! tace."Ban sani ba."!! Kashe wayar tayi tana tsaki sai numfarfashi take na takaici da 'bacin rai!

Dariya yay mai yawa kafin ya ajiye wayar ya nufi toilet cikin wani irin farin ciki wanda ya jima be tsinci kansa a ciki ba.

*'DAURIN AURAN* Ya samu halartar manyan mutane sarakai 'yan kasuwa da manyan 'yan siyasa daga kowace jaha, daurin auran yayi albarka da yawa daga cikin mutanan da suka halarci daurin auran sunyi mamakin rashin halartar angon, sai dai Asp beyi kasa a gwiwa ba gurin sheda musu halin da ake ciki, hakan yasa wa'inda ba su sheda da UMAR din ba suka sheda dashi da jamurtarsa amma mafi akasari jama'a sun san shi a hoto da kuma gidajen television................ Asp bai samu kansa ba sai da ya tabbatar da cewa yasa jama'ar da suka samu damar hallatar daurin a auran a mota, da yawa daga cikinsu 'yan uwan UMAR din ne da suka dinga turereniya gurin zuwa daurin auran. wanda aka daura a garin KANO a fadar

maimartaba Sarkin gari..

*Kika futar min da littafi keda Allah!  ki ka karanta baki biya ba kema keda Allah!*

*#500via.....0542382124.....Binta umar gtbabk, idan kati zaki turo  kiyi min magana ta WhatsApp da wannan number.... 07084653262.....BINTA UMAR ABBALE*
[2/1, 11:07 PM] Matar Malam: _Ina muku tallan group dina mai suna_
*MAR'ATUSSALIHA*
*Wanda na bude shi wata shida da suka wuce a lokacin 1k ne kudin register,  yanzu saboda yanayi na rayuwa yasa na mayar dashi #500  za kiyi register domin kasancewarki cikin group din, matan aure da zawarawan dake shirin aure da 'yan mata masu shirin aure ku nake da bukatar kuyi  rigstar domin k'aruwarmu baki d'aya, akwai sirri da amana a tsakaninmu, duk wata matsalar dake damunki ki sameni ta pravite insha Allah zan baki shawarwari wanda zasu taimaka miki domin gyara kanki da zamantakewar auranki,  'yar uwa kiyi register da group din MAR'ATUSSALIHA Insha Allah zaki samu mafita.......ga duk wacce take da bukatar biyan kudin 0542382124....Binta umar gtbank sai ki tura kudin ta wannan account din ki tura min sheda ta wannan number... 07084653262*

*51&52*
Fitowarsa daga wanka yayi dai-dai da shigowar kira a wayarsa, koda ya  dauki wayar ya duba sai yay murmushi domin ganin sunan  wanda yake tsammani a fuskar wayar

Yasa wayar a kunnanshi  tare da sallama a bakinsa.

Daga daya bangaran Asp ya sauke ajiyar zuciya da fadin."Alhamdulillhi komai ya kammala an daura aure cikin farin ciki da mutunta juna kowa ya kasance cikin walwala da farin ciki, bayan haka daurin auran ya samu halartar  manya mutane daga kowane sassah na kasar nan, anyi taro an tashi lafiya duk jama'ar da suka samu damar halartar daurin auran daga b'angaran ka kama daga 'yan uwa da abokan arziki da kuma yaran ka  yanzu haka suna kan hanyarsu ta komawa gidajensu da ikon Allah, muna rokon Allah ya bada zaman lafiya a cikin wannan auran sannan ya mayar da kowa gidansa lafiya."

Numfashi ya sauke bayan k'are maganar Asp din yace." Na rasa da wane baki zan mika godiya ta a gare ka, hakika ka cika mutum wanda ya tara duk wasu abubuwan da ake da bukatar mutumin 'kwarai ya kasance, wallahi wayewar yau haka  kawai na tsinci kaina wani irin farin ciki wanda na kasa tantance ko na menene?  bana gari ina wata uwa duniya ka tsaya min akan muhimmin al'amarin da cancanta ace ni nake tsaye a kansa, Asp da izinin Allah ba zan baka kunya ba,  yanda ka tsaya kai da fata kaga tabbatuwar al'amarin nan, to nima nayi maka

alkawari zanyi iyakar bakin kokarina gurin ganin na zauna lafiya da yarinyar nan, kafi karfin komai a gurina,  duk irin kin al'amarin nan da nake tunda ka shiga cikinsa dole nayi mubaya da kai da abunda kake so nagode sosai da sosai Allah ya saka da alkairi ya bar mana zumunci."

Murmushi yay da fadin." Haba babu komai wannan ba wani abun damuwa bane, dama ni fatana ka yarda ka amince dari bisa dari da wannan auran, domin haka kawai nake maka sha'awar auran yarinyar duk da a zahiri kai ka nuna cewa ba irinta kake da bukata ba, wannan dalilin ba zai ha naka nan gaba ka auri wacce zuciyarka take so ba tunda kana da damar hakan, nagode sosai da yanda kake mutuntani kana kar'bar shawarwarina daga karshe nake sake yi maka fatan alkairi da samun zuria dayyiba."

Cikin jin dadi ya amsa da ameeen ya rabbi Allah ya saka da alkairi mutumina."

Cikin  zolaya yace."Yanzu zan shiga cikin gidan domin samun dauko maka hoton amaryar taka ko baka da bukatar hakan."?

Hannu yasa ya dan sosa sumar kanshi kafin yayi dan murmushi irin wanda ya saba, yace." Ina da bukata mana, ba kaji bahaushe yace."Amarya ko tabuzuzu ce tana rike da kambutan sarauta ba to ballantana ita wannan *GIMBIYA* ce mai lasisi wallahi  haka kawai naji ina so nayi tozali da ita."

Asp ya kyalkyala da dariya da fadin." Allah mutumina ai dama ni na san duk wannan abun da kake iya fatar baki ne kana son yarinyar nan kawai ba zaka fito fili ka nuna ba."

Shima yana dariyar yace."Haka dai kake hasashe amma ni yar hanzu bana jin sonta a cikin zuciyata."

Yace."Okey to shikkenan mu bar wannan maganar amma ni na san akwai ranar da tarihi zai maimaita kansa."

Shuru yay bece komai ba har yanzu  da kyakykyawan murmushi a fuskarsa sai wani sosa sumar kanshi yake kamar wani mara gaskiya.

Asp din yace."Zan kashe waya zuwa an jima zaka ji ni."

Yace."Okey to shikkenan babu damuwa sai na jika din." Sallama sukayi da juna kafin kowa ya kashe wayarsa.

To a can gidan Uwale kuwa hayaniya ce kawai take tashi tun bayan dawowar mazan daga gurin daurin aure suka taru a gidan tare da sauran 'yan uwansu mata kowa na fadin albarkacin bakinsa.

Da yawa daga cikinsu sun ji dadin kasancewar al'amarin, amma kuma akwai wa'inda suke ganin kamar hakan cin fuska ne da kuma rashin adalci idan akayi duba da irin halarcin da Hamra'u tayi masa bai cancanta ace  saboda yayi arziki ya samu duniya ya juya mata baya ba, ita ya kamata ace ya fara aure kafin wata mace.

Uwale da yake tana da hankali da tsinkaye ta dinga nusar dasu domin su fahimci cewa shi UMAR  din bashi  da laifi domin yarinyar bashi akayi ba wai don yayi arziki zai guji auran ita Hamra'un ba, kuma ya tabbatar mata da cewar zai auri ita Hamraun a matsayin matarsa ta biyu...........Duk da wannan bayanin da tayi musu hakan besa hankalinsu ya kwanta ba domin ita mahaifiyar Hamra'un ma kasa zama tayi a gidan rai a bace ta tattara 'ya'yanta suka tafi........'Bangaran Ita  Hamra'un, abun babu dadi domin tun waye war garin ranar take kuka duk ta tsangwami kanta da kanta gani take kamar bukatarta ba zata biya ba , haka kawai take tsoron hada  kishi da 'yar sarautar tun ganin farko da tayi mata jikinta yay sanyi! 'Kawarta Zabbah da tazo ta sake rikirkita ta da cewar had'a kishi da 'ya'yan sarauta bala'i ne domin basa barin kishiyarsu ta zauna lafiya babu wanda be san gidan sarauta da asire-asire ba, saboda haka dole itama sai ta tashi a tsaye mutukar tana so bukatarta ta biya.

'Bangaran uwar Hamra'un ma maganar da suke tattaunawa kenan da yar uwanta, inda suke zuga ta kan cewa lallai dole ta tashi a tsaye domin ganin 'yarta ta auri UMARU idan ya kama tabi malamai a kansa ba damuwa bace tunda duk wani abu da akayi masa shi ya janyo dalilin rashin adalcin da yayi musu, idan ba haka ba mai zai sanya yaje ya auri wata bayan kowa ya san abinda yake tsakaninsa da Hamra'u,  ta bauta masa sosai ta kori duk masu neman auranta akansa, ta zauna zaman jiransa, rana tsaka saboda yayi arziki zai je ya auri 'yar sarauta, ya wulakanta yarinyar da tayi masa halarci, wannan dalilin yasa suke zugata kan cewa lallai ta nemi taimako a gurin malamai domin janyo hankalinsa, idan kuma ta zauna to tana ganin daula da jin dadi zasu wuce 'yarta wacce akayi gwagwarmar tare da ita.

Sosai Dayyiba mahaifiyar Hamra'u ta dauki hudubar 'yan uwanta tasa a zuciyarta cewa gobe zakara ne zai bata sa'a  yo ita da take a cikin garin Katsina to me zai gagareta, akwai malamai iri-iri wa'inda zasu taimaka mata, duk asirin da ake fadi cewa gidan sarauta suna dashi, to ita ta dauki alwashin bugawa dasu.

Tofah!!!🤔

*****

Yayi ta tsumayin Asp din shuru be turo masa hotonan ba, agogon dake daure a hannunsa ya duba awa biyu kenan da wayarsu, ko wane irin hoto ne yaci ace an dauka ya turo masa haka kawai ya 'kagauta ya kalli  kwalliyar amaryar tasa.

Number sa ya nemo ya kira cike daso ya daga wayar, sai duk 'kagautarsa bai samu abunda

yake so ba, domin wayar haka ta k'araci 'burari Asp din be daga ba.

'Karamin tsaki yaja tare da dan ya mutse fuskarsa, ya ga alama fa zuciyarsa ta nema ta takura masa.

Ajiya wayar yayi, ya dauki d'ayar dake saman drowar yana kunnawa ya shiga WhatsApp number tace kawai data Asp a layin.

Ya duba status Asp ya dora hotonan daurin auran........Jama'a birjik babu masaka tsinke harabar gidan sarautar cike da jama'a, murmushi kawai yake yana cigaba da duba status din.......... Kowa ya halarci daurin auran a cikin abokan aikinsa da 'yan uwansa da kuma yaransa su Alba da sauransu. hoton karshe shine Maimartaba Omar tare da maigirma Governor katsina wato Nasiru Alkanawi dashi Asp din da kuma mutuminshi abokin fad'ansa wato Commissioner of police wato Murtala Kabiru, serving din hoton yay a ajiye a gallery hoton yayi masa kyau sosai.

Yana k'okarin sauka sak'on ta ya shigo, da sauri ya shiga yana dubawa hotonta ne kusan goma ta turo masa.

Ya dinga duba hotonan d'aya bayan d'aya yana jin wani bala'in kishi na sukan zuciyarsa.

A zahiri dai shi ta turowa hotonan, amma a cikin rashin sanin ta, sai kawai ya tsinci kansa da jin haushin kansa da kuma kishin kansa da kansa.

A zahiri shi ya kamata ace ta turowa hotonan a matsayinsa na miji a gareta. amma ta turawa wani wanda bata da tabbas a kansa, wannan ya nuna masa cewa zata iya aikata komai bayan da auransa a kanta.

Zazzafar ajiyar zuciya ya sauke kafin ya dauki daya daga cikin hoton nan data turo masa yay magana a kansa.

"Wannan hoton yayi kyau sosai my love kallonki a yanzu ya jefe ni cikin wani hali mai wuyar fassaruwa, gabadaya kin gama kashe min jikina ina jin sha'awar kasancewa dake a halin yanzu, my lov ina kishin wannan mijin naki kada ki bari ya kusanceki ballantana wata mu'amula ta shiga tsakaninku, ki rike min amanar kanki."

Koda ya tura mata sakon be sauka ba har sai data ta duba, ba tace masa komai ba sai emoji data tura masa mai dauke da alamar kuka da ban hakuri.....Daga haka sai kawai ta sauka,

Cikin jin haushin abinda tayi ya kashe wayar ya ajiye yana nazari da tunani akan al'amarinta.

Kiran sallar la'asar ne ya katse tunaninshi, da sauri ya tashi ya nufi toliet domin daura alwala. koda ya fito daga bandakin kai tsaye masjid ya nufa wanda yake cikin barrack din da suke zaune........Da yawa daga cikinsu arna ne musulman cikinsu kadan ne, amma duk da hakan akwai kyakykyawar alaka a tsakaninsu domin tsayin kwanakin da yayi tare dasu bai ta'ba samun matsala da kowa ba.

Bayan fitowarsu daga masjid din Adewale abokin aikinsa wanda ta su tazo daya ya tsare shi da hira, hakan ya zauna ya biye masa yana ta bashi labarin ban dariya cikin harshan turanci yake magana domin hausar tashi bata fita sosai.

Kwanakin da yayi a cikinsu gami fa cud'anyarsa dasu yasa kwakwalwarsa ta kara bud'ewa dama can sama-sama yana jin turacin amma ba kamar yanzu ba, ya na ji sosai kuma idan ta kama yana sauya harshe yayi magana tamkar wanda ya jima a cikinsa.

Adewale mutum ne mai barkwanci shiyasa tasu tazo d'aya duk sanda basu da aiki sukan zauna guri daya yay ta sauraran shiremansa yay ta kyalkyala dariya kamar bashi ba.

Kiran Asp ne ya shigo wayarsa yasa a kunne tare da sallama Asp din yace."Ka duba tuntuni na tura maka sakon."

Yace."Okey to ina godiya sosai naje sallah shine dalili." Yace."Ba damuwa yanzu Ina shirye-shiryen d'auko hanya amma ina tsammanin jirgi zamu bi."

Yace." Saboda me? zaku bi jirgi ina Kano ina Katsina ? da har sai kun shiga jirgi."

Yace." Wannan amaryar tamu ai daban take da sauran mata, idan da akwai abunda yafi jirgi to a ciki zan kawo maka ita har Katsina."

Yayi yar dariya da fadin." Kana d'aurewa karya gindi wallahi, amarya babu ango a kusa ina tausaya mata kwanan kad'aici."

Asp din yay dariya sosai kafin yace."Ka fara tausayawa kanka kafin ka tausaya mata dukkaninku ababan tausayi ne."

'Yar dariya yay irin wacce ya saba da fadin'' Na yarda da maganarka amma ka mi'ka min sak'on gaisuwata a gurinta ka sheda mata cewa daga yau ta fara lissafin dawowata."

Yace."Wannan kuma aikin ka ne, domin saura kadan na kammala nawa, sauran kuma ya rage naka."

Kokarin magana yake Asp din ya kashe wayar

Ya cire wayar daga kunnansa yana murmushin da har yanzu ya rasa na menene.

Yana duba hoton nan Adewale ya leko da kansa.

Da sauri ya janye wayar don haka kawai yake jin kishin wani ya ga kwalliyarta.........duk da hakan  sai da ya hangota, ya kyakyala da dariya yana sake le'ka kansa da fadin."Oga wannan yarinyar fa tana da kyau sosai ina san 'bakar mace domin tana da wani sirri na daban."

Wani irin kallo yay masa mai kama da harara kafin yaja karamin tsaki yasa wayar gaban aljihun rigarsa ya mike da fadin." Kai matsala ta dakai shiririta haka kawai daga ganin matar mutane kace kana so Adewale kana da son mata wallahi."

Yace."Ai sune jin dadin duniyar Oga hahahaha." Ya k'arashe maganar cikin dariya.

Girgixa kai kawai yay yana kallonsa da tarin takaicin shirmen da yake yace." Ni zan shiga ciki na huta kafin magriba domin naga alamar yau shirmen naka yafi na kullum."
Shima tashi yay da fadin." Nima ina da uzuri yanzu zanje na gabatar sai mun hadu da daddare."
Hannu ya daga masa kawai, yana kallonsa yayin da yake kokarin barin gurin.

Kansa kawai ya girgiza kafin shima ya bar gurin cike da so ya samu zama a nutse domin samun damar  kallon hotonan amaryar  tashi a tsanake.

*Kika futar min da littafi keda Allah!  ki ka karanta baki biya ba  kema keda Allah!*

*#500via.....0542382124.....Binta umar gtbabk, idan kati zaki turo  kiyi min magana ta WhatsApp da wannan number.... 07084653262.....BINTA UMAR ABBALE*
[2/2, 11:06 PM] Matar Malam: _Ina muku tallan group dina mai suna_
*MAR'ATUSSALIHA*
*Wanda na bude shi wata shida da suka wuce a lokacin 1k ne kudin register,  yanzu saboda yanayi na rayuwa yasa na mayar dashi #500  za kiyi register domin kasancewarki cikin group din, matan aure da zawarawan dake shirin aure da 'yan mata masu shirin aure ku nake da bukatar kuyi  rigstar domin k'aruwarmu baki d'aya, akwai sirri da amana a tsakaninmu, duk wata matsalar dake damunki ki sameni ta pravite insha Allah zan baki shawarwari wanda zasu taimaka miki domin gyara kanki da zamantakewar auranki,  'yar uwa kiyi register da group din MAR'ATUSSALIHA Insha Allah zaki samu mafita.......ga duk wacce take da bukatar biyan kudin 0542382124....Binta umar gtbank sai ki tura kudin ta wannan account din ki tura min sheda ta wannan number... 07084653262*

*53&54*
Pictures din data tura masa a rashin sanin shi ta turawa,  sun bambamta da wanda Asp din ya turo masa a yanzu,  wanda ta  tura masa a yanzu tayi  ado  sosai sa'banin wanda ta tura masa

adon da tayi bai kai na yanzu ba,  Ies din ne dai a jikinta amma kamar yafi na dazu kyau da kudi, riga da siket ne dinkin ya karbi jikinta sosai tai kyau tai ado da gold wuya da hannu sai tai amfani da set din jaka da takalmi da mayafi iri daya, mayafin a gefen kafada ta ajiyeshi, duk jikinta a waje breast dinta sun matse a cikin rigar don har sun dan fito daga sama,  kishin hakan ya dinga sukan zuciyarsa ya cigaba da kallon hotonan wanda duk rabinsu ita da 'yan uwanta ne maza da mata sai kuma wanda Asp din ya shiga akayi musu ita dashi,  shi kansa Asp din haushi ya bashi ya dinga jin  kishinsa  a ranshi,  ganin yanda ya tsaya daf da ita bayan duk ga tsaraicinta nan a waje a maimakon yay mata magana ta yafa mayafinta  tunda dai su 'yan uwan nata basu san abunda ya dace ba, shima sai  yabi sahun su suna abunda bai dace ba........'Karamin tsaki yaja ya cigaba da duba hotonan yana kokarin danne abunda ke cin zuciyarsa.

hoton ta  ida Sakina shine ya dauki hankalinsa, kallon fuskar Sakinar da shigar dake jikinta shi kadai ya nuna masa zahirin ta,  duk rashin arzikin dinkin dake jikin Zinat din yafi na ita Sakinar mutunci, domin gabadaya wuyar rigar dake jikin Sakinar net ne nonowanta duk sun fito gashi rigar ta matseta  sosai  ba mayafin arziki a jikinta sai wani uban gashin doki  da tayi ado dashi, gabadaya kamar ba 'yar musulmai ba..........Murmushin dake kan fuskokinsu shine ya nuna masa cewa da akwai kusanci  mai kyau a tsakaninisu domin hannuwasu ma a rike yake dana juna.........Gabadaya yarinyar bata kwanta masa a rai ba,  ba tare da ya gama kallon hotonan ba, ya kashe wayar ya ajiye saman drowar  haushi duk ishe shi.

Koda Asp din ya kira shi domin  ya  shada masa  cewa suna jirgi shi da amaryar tasa,  sharrin zuciya sai kawai ya tsinci kansa da jin  wani iri  a ranshi,  sai da yayi namijin kokari kafin ya iya yi masa godiya, Asp din yaji muryarsa a dakile, yace."Mutumina ya akayi ne naji ka wani iri."?

Ya dan yi gyaran murya da kokarin kawar da abunda yake ransa yace."  Normal ba matsala idan kun sauka  ka kira ni yanzu ina dan uzuri ne."

Yace."Okey to shikkenan  ko na baka amaryar ne."?

Girgixa kai yay da fadin." Aa bar ta kawai zan kira ta an jima idan ta huta." Yanda  yake jin haushinta  ya san ba zasu wanye lafiya ba, shiyasa ya fadi haka.

Wayar ya kashe ya ajiye saman drowr ya tsirawa kasan kafet ido.

Alamu sun nuna yana son yarinyar nan, domin da baya sonta ba zai damu kansa har ya dinga kishi a kanta ba.

Asp yafi karfin komai a gurinsa, kuma ya sheda cewa ba zai ci amanarsa ba, amma yana mamakin yanda zuciyarsa take raya masa wasu munanan abubuwa akan Asp din  wanda yayi

imani da cewa hakan ba zata faru ba, auziyya yayi a fili tare da korar shaidan din da yake so lallai sai ya nuna masa aibun abokin nasa.

Hadiman ta wato masu yi mata hidima tare da motocin kayan garar da akai mata sune suka fara sauka, duk girman store din sai da yay kadan gurin daukar kayan garar, babu abunda babu na dangin ci da sha, da store din ya cika sai kawai aka jibge ragowar kayan abincin a harabar gidan.

Asp sai da ya tabbatar da cewa komai ya kammala amarya na dakinta sannan hankalinsa ya kwanta ya godewa Allah kafin ya kira wayarsa ya sheda masa duk abunda yake faruwa.

Yace."Asp nifa ban bukaci komai a gurinsu ba, me zai sanya akawo min abinci ina dashi ai ba wai ina bukata bane."

Yace."Al'ada ce kawai  kada ka damu ba wai dan ka gaza ko don baka dashi sukayi maka haka ba alkairi ne kawai."

Yace."Idan za suyi  ai sai ayi dai-dai gwargwado amma ace har mota goma ta kayan abinci me zanyi dasu mybe ma kafin azo kan wani ya lalace kawai ka diba iya wanda kake bukata, sauran kuma zanyi magana da Uwale domin ta bawa wanda ya dace."

Yace."Hakan da kayi yayi dai-dai, amma ni kam babu abunda zan dauka acikin wannan kayan, akwai mabukatan da suke nema su ya kamata a rabawa.

Yace."Shikkenan tunda kace haka idan akwai masu bukata a bangaran ka sai ka basu duk abunda ya dace."

Yace."Okey babu damuwa zan duba insha Allahu.

Godiya yayi masa sosai tare da ban gajiya kafin suyi sallama da junansu.

Tun bayan fitar Asp din daga gidan, take bin dakin da kallo, duk iya hangenta bata hango abunda zata kushe a dakin ba, daga bedroom din har falon komai na kasar  waje ne,  kuma tsarin yayi mata babu abunda zata nema komai a kwai wanda zata bukata, toilet biyu d'aya a uwar daki d'aya kuma a falon, sai kicin dake can gefe a dai cikin falon, koda ta duba kicin din shima a shirye yake da komai na bukatar yau da gobe, hakan yayi mata dadi dama bata bukatar wani ya shiga sabgarta a gidan idan ba hadimanta ba.

Ta gama duba ko'ina ta koma bedroom din ta zauna gefen gado tare da zabga tagumi, to yanzu fa wata sabuwar rayuwa za tayi tare da wasu sabbanin mutanan da bata san ya hallinsu yake

ba, koda yake a shirye take da kowa duk wanda ya bukaci zaman lafiya da ita bata da matsala amma ba zata yarda da raini daga gurin kowa ba ciki kuwa harda wanda yayi dalilin zuwanta gidan.

Ajiyar zuciya ta sauke tana tunanin akan irin zaman da za tayi da bagidajen mijin nata. Tsaki taja mai tsayi ta girgiza kai a fili tace." Idan yaso mu zauna lafia zamu zauna idan kuma yazo da tsiya to gidan ya tarar domin ba zan yarda da rainin hankali ba." Kamar dashi take maganar sai girgiza k'afafu take.

Kiran wayarsa ne ya katse tunaninta, data duba taga shine sai taki d'aga wayar har sai da ta katse.

Uzuri yay mata dan be kawo cewa iskanci ne ya ha nata daga masa waya ba.

A karo na biyu sai da ta kusa katsewa ta daga, ciki ciki tai sallama.

Be damu da abunda take ba ya amsa mata da fadin." Ya kike? ya kuma hidima da jama'a."?

Shuru tai ba tace masa komai ba.

Yace."Kin yi shuru ko baki da magana dani."?

Ta dan ya mutse fuska da fadin." Umm! yanzu bacci na keji okay sai da safe." Kokarin kashe wayar take yay saurin fadin." Kada ki kashe waya ina da magana dake."

Ta fasa kashe wayar da fadin "Ina jin ka."

Jim yay kafin yace." Kina ina yanzu."? tambayar da yay mata kenan

Tace."Wace irin tambaya ce wannan."?

Dan murmushi yay kafin yace." Ke dai ki bani amsar tambayata."

Tsaki tayi niyyar ja, sai kuma ta fasa tace."Abokinka ya kamata ka tambaya ai."

Yace." Tun dazu nake kiran wayarsa bata shiga shine dalili.

Tace." Okey to gani yanzu a cikin gidanka zaune daki."

Ajiyar zuciya ya sauke da fadin." Alhamdulillhi dama abunda nake so naji kenan daga bakinki."

Numfashi ya sauke kafin ya cigaba da cewa." Da bakin ki yanzu kike sheda min cewa kina cikin

gidana zaune a daki a matsayin  matata ta sunnah,  bana gari anyi komai an gama duk ta dalilin jajurcewar abokina wanda ya tsaya min a cikin al'amara na, Asp hankalinsa bai kwanta ba sai da ya tabbatar da cewa kin zama mallakina  bayan haka kuma be samu nutsuwa ba sai da ya tabbatar da cewa ya kawo ki har cikin  dakinki ya ajiyeki kamar yanda ki ka sheda min a yanzu.

Ina so ki san cewa ni mutum ne mai tsananin kishi akan abuna, duk da ga yanda akayi wannan auran namu cewa bana so bakya so hakan ba zai sa na zuba miki ido kiyi abunda ki ke so ba.........Katse shi tayi ta hanyar fadin." Me kake nufi ne."?  Yace ." Alkairi nake nufi dake."? Shuru tai ba tace masa komai ba amma ya fara kai ta karshe........Ya cigaba da cewa." Yanzu sabuwar rayuwa zakiyi domin aure ba wasan yara bane. Ki kiyaye mu'amula da wanda bai dace ba, kada kiyi mamakin cewa ina can wani gari amma labarin halin da kike ciki zai sameni har lokacin dawowata gida, ki goge  number duk wanda kika san cewa ba muharramin ki bane kafin na dawo,  sannan ban yarda kije ko'ina ba, akwai securities da zasu sheda min shigarki da kuma fitarki.   idan kina da wata Matsala kina iya shedawa Asp domin dashi kadai na yarda bayan shi ban yarda  wata magana ta shiga tsakaninki da ma'aikatan gidan nan ba, wannan shine abunda nake so ki rike a ranki kuma kiyi aiki da umarni na."

Wani bacin rai ne ya tsaya mata a wuya jin yanda yake mata magana cikin isa da gadara kamar wani ubanta, koda yake tunda aka daura auran iyaye da kakanni ke mata nasiha cewa tabi mijinta sau da kafa domin tunda ta riga ta bar hannun iyayenta to basu da hakki mai karfi a kanta kamar yanda mijinta yake da hakki a kanta, dole ne ta bishi ta kuma bi umarninsa, yi nayi bari na bari wannan sune irin nasihohin da aka dinga yi mata kafin kawo ta dakin mijin nata shi kansa Maimartaba fada yay mata sosai akan biyayyar aure...............Ita kuma sai take ganin kamar  wannan shine dalilin da yasa su mazan suke nuna izzah! da gadara! akan matayensu saboda wannan damar da Allah ya basu,   gashi dai  ita ko kwana daya ba tayi ba a gidan ya fara kafa mata sharud'ai bayan ma baya garin amma yana nuna mata isa da mulki saboda kawai yana wasu tunane- tunane marasa kyau a kanta,  Ajiyar zuciya ta sauke tare da kokarin danne bacin ranta tace." To i dan ka gama maganar ka  zan kashe wayata."

Ashe  maganar  banza take domin tuntuni ya kashe wayarsa ya bar ta da tata a kunne sai kace shashasha.

Cire wayar daga kunnanta yayi dai-dai da zubar hawaye da take kokarin dannewa.

Ta jefar da wayar saman gado ta  dafe kanta da duk hannuwa biyun kukan takaici ne ya kufce mata!

Hakika an kassara mata rayuwa  tunda har  aka had'ata aure da  bagidajen namiji wanda bai iya lallashi da lallami mace ba, kullum bakar magana ce take shiga tsakaninsu,  ya za'ayi ta iya zaman aure dashi a haka,  burin ta a rayuwa ta auri namijin da ya iya soyayya da kula da mace sai gashi ta b'ige da auran bahagon mutum wanda ya rako maza duniya.

Ta jima tana share hawayen takaici kafin ta cire kayan jikinta ta nufi bandaki domin watsa ruwa a jikinta.

Lokacin da ta fito yayi dai-dai da shigowar Uwale dakin, suna hada ido sai tayi saurin kawar da kanta tana ya mutse fuskarta, kai tsaye dressing mirror ta nufa.

Uwale jikinta yay sanyi domin ta lura da irin kallon banzan da tayi mata.

Ta nuna kamar ba ta gani ba da 'yar fara'a tace."Sannu yarinyar arziki dama na shigo ne na dubaki sannan na tambayeki ko da akwai abunda ki ke bukata, ga dai abinci can a falo ajiye miki."

Uwale tafi minti biyar da gama maganar amma ko kallonta ba tayi ba ballantana ta samu damar bata amsa, sai kawai ta juya jikinta a sanyaye ta bude dakin ta fita tana mamakin rashin tarbiyar yarinyar.

Tana fita taja tsaki ta cigaba da shafa mai a fatar jikinta daga shi har kakar tasa haushinsu takeji.

A sanyaye ta zauna kan kujera jikinta duk babu karsashi.

Hamra'u ta kalleta da fadin." Uwale ya naga kin dawo da jiki a sa'bule."?

'Yar dariya tayi da fadin." Aa ba wani abu ne ai Gimbiyar tayi bacci lokacin dana shiga gurin nata."
Cikin rashin so ta bayyana mata abunda ya faru ta k'arasa maganar.

Tai 'yar dariya da fadin." Uwale kenan, jikina na bani akwai wani abu da ya faru amma tunda kina boye min shikkenan."

Da sauri tace." Ke 'yar nan me zai faru kuma idan ba alkairi ba? ni babu wani abu da yarinyar nan tayi min koda na shiga na sameta tana bacci sai kawai na fito nace idan Allah ya kaimu da safe sai mu gaisa da juna kawai kuma sai ki zargi wani abu."

Yanda take magana da son kare Gimbiyar sai ranta ya baci kishi yasa ta ta'be baki tare da mikewa da fadin." Ni zan shiga na kwanta sai da safe."
Ta bita da kallon nazari kafin tace."Allah ya tashemu lafiya." Da sauri ta bar gurin ranta a masifar b'ace, Ta rasa gane mai yake damun Uwale, tunda Gimbiyar ta sauka a gidan ta rasa nutsuwarta sai kai kawo take tsakanin kicin da falo da kanta ta shirya mata abinci mai dadi irin na tsofaffin hannu, duk tana zaune tana kallonta tana rawar jiki ta dauki abincin domin ta kai mata, sai gashi kuma ta dawo da jiki a sab'ule, tabbas wani abun ne ya faru amma wai sai take 'boyewa mata kome menene dalilin hakan oho! ita kam tayi alkawari cewa ba 'yar sarauta ba

ko wacece ita wallahi tayi rantsuwa cewar ba zata bauta mata ba,  tunda dai ba zaman ta take a gidan ba, itama Uwalen  itace  ta d'orawa kanta wahala amma ita kam duk rintsi  ba zata yarda ayi  haka da ita ba.

*Kika futar min da littafi keda Allah!  ki ka karanta baki biya ba kema keda Allah!*

*#500via.....0542382124.....Binta umar gtbabk, idan kati zaki turo  kiyi min magana ta WhatsApp da wannan number.... 07084653262.....BINTA UMAR ABBALE*
[2/4, 3:24 PM] Matar Malam: *55&56*
Kayan bacci masu taushi ta sanya a jikinta, babu wani kuzarin kirki a tattare da ita,  ta kwanta kan gado tare da jan bargo ta rufe jikinta. Ido ta rintse bacci kawai ta keso tayi ko ta samu saukin 'bacin ran da ya addabeta a zuciyarta, amma duk yanda taso  ta  gayyaci baccin yaki zuwa,  idonta tar mazai! har yanzu tana tunanin kausasan kalamansa a kanta, a mafarki bata ta'ba tunanin cewa za tayi irin wannan auran ba, duba da yanda ta dinga katantanwa da tarin maza masu mulki da mukamai daban-daban wanda  suka mace a soyayyarta. Tabbas maganar Sakina gaskiya ne in da take cewa a lokacin da kake dama ya kamata ka dama,  idan ba haka ba,  to wanki hula zai kai ka ga dare, yanzu wa gari ya waya gashinan ta 'bige da auran namijin da bata ra'ayinsa...........Idonta a lumshe take wannan tunanin tana kuma hasaso fuskar b'oyayyan masoyinta wanda take jin bala'in sonsa a cikin zuciyarta saboda soyyarsa da kuma iya kalamansa,  shi kad'ai ne a yanxu zai kawar mata da b'acin ran dake damunta,  amma kuma haka kawai a zuciyarta take jin tsoron kiran wayarsa.  zazzafar ajiyar zuciya ta sauke ta dan gyara kwanciya tana takure jikinta guri guda  kamar me jin sanyi koda yake hakan nan  ta tsinci kanta cikin wannan halin duk sanda za ta kwanta bacci   ta dinga juye-juye kenan kafin baccin ya dauketa  sai an ja dogon lokaci tukkuna, daga nan kuma sai ta dingi mafarkai barkatai! masu kyau da marasa kyau har sai garin Allah ya waye tukkuna, za ta tashi cikin tsananin sha'awa domin duk yawanci mafarkan akan sex ta keyi  alhalin sam bata kwanciya da abun a ranta, wannan dalilin yasa tayi alkawarin cewa duk  magungunan matan da Aunty's dinta sukayi mata guzurinsa ba zata sha ko daya ba domin ta riga ta d'ora  zarginta  kan cewa duk magungunan data dubga dalili,  saboda da can ba haka take ba, duk yawan shekarunta bata ta'ba  mafarkin wani da namiji ba sai gashi kullum idan ta kwanta sai tayi mafarki gata dumu-dumu da namiji suna sex  yana biya mata bukata.

Bargon dake rufe a jikinta ta sake gyarawa  kafin  k'ira ya shigo wayarta dake saman bedside, cike da mamaki ta dauki wayar tana dubawa  ashe bata kashe ba ta kwanta.

Sunan 'boyayyan masoyi ne yake yawo kan fuskar wayar.

Gabanta ya dinga faduwa ta shiga nazari da  tunani akan ta daga wayarsa  ko kada ta

daga..........*"Ki goge duk  number wanda ki kasan ba muharramin ki bane kafin na dawo, kada kiyi mamakin cewa duk halin da kike ciki zan samu labari saboda haka  ki kiyaye kuma kibi umarnina."*  Manganganunsa suka fad'o mata a rai,  ta tsirawa fuskar wayar do tana kallo har ta katse.

Ya sake kira still dai bata daga ba, sai bin dakin take da kallo tana tunanin ko da akwai wata na'ura da ya daura a dakin domin ganin duk  motsinta.............haka kawai take jin tsoron ya kamata da wani laifi mussaman irin wannan ba wai don tana tsoronsa ba, yanda ta lura dashi kamar shima yana zargin ta irin yanda wasu daga cikin jama'ar gari suke mata abunda ta tsana kenan a zarge ta akan fasikanci,  wannan shine dalilin da yasa take jin tsoron daga wayar boyayyan masoyin nata.......Sai kawai ta yanke shawarar shiga whasp ta duba ko ya ajiye mata sako.

WhatsApp ya shiga domin har yanzu ya kasa  yarda da abinda zuciyarsa take raya masa a kan yarinyar zai cigaba da gwadata har sai ya fahimci in da ta dosa.

Yaji dadin ganinta a online  sai ya tura mata sako kamar haka.

_My love me yasa baki daga waya ta ba."_?

Ta bashi amsa kamar haka"

_Ai ba muyi da kai cewa zaka dinga kiran  waya ta  ba, idan hakan ma ta kama cewa nayi ka bari ni zan kira ka, to mai zai sanya ka kira ni a irin wannan lokacin."_

Yace."
_My love  menene a ciki  don na kira ki na debe miki kewa, na san da cewa angon naki baya gari shiyasa nake so na debe miki kewarsa._

Emoji ta tura masa na mamakin maganarsa.

Yace." _Kin san irin son da nake miki ne yasa nake bin diddigin duk abinda ya shafe ki mijin baya gari yana gurin training ko ba haka bane."?_

Murmushi takaici tayi kafin ta tura masa da amsa.

_"Eh hakane maganar ka amma nayi mamakin yanda akayi ka san haka."_

Yace." _Kada kiyi mamaki da  sanina halin da kike ciki, ko kin manta nima d'an cikin garin

katsina ne, ai shiyasa ban cire tsammanin had'uwa dake a kurkusa ba tunda muna cikin gari daya._

Amsa ta bashi kamar haka..
_"Faruk ina sonka sosai irin wanda ban ta'ba yiwa wani namiji ba,  hakika zan so na ganka a zahiri sai dai wannan mijin nawa yana da zafi! kuma ma'aikacin tsaro ne ina jin tsoron ka shiga hannunsa ba za kaji dadi ba._

Murmushi yay lokacin da ya karanta sa'kon  ya gyara kwaciyarsa kafin ya bata amsa kamar haka.

_"Na san da haka my love bana tsoron had'uwa  dashi ballanatana naji tsoron gwabzawa dashi ina mai tabbatar miki da cewa a kanki babu abunda ba zanyi ba,  zan iya fansar da raina akan soyayyarki  ina so ki cire tsoro a cikin zuciyarki, ki cigaba da kokarin ganin kin rabu dashi kizo gare ni muyi aure,  ni nayi alkawarin baki dukkanin kulawar da kike bukata."_

_Cikin jin dadin maganarsa tace."Nagode sosai wannan manganun naka sun kashe min jiki wallahi na rasa abinda zance maka nagode sosai da kulawarka kuma nayi maka alkawari cewa zanyi  kokarin ganin mun hadu da juna, kada ka damu bukatarmu ta zata biya da izinin Allah."_

_Yace." Nagode my love yanzu me kike bukata nayi miki wanda zai faranta ranki."?_

Shuru tayi bata iya ce masa  komai ba, gabadaya ya gama kashe mata jiki da salon soyayyarsa.

Ganin tayi shuru ba tace masa komai ba kuma yana ganinta a online bata sauka kawai ba tare damuwar komai ba ya tura mata sticks  masu tayar da hankali gami da tayar da sha'awa mussaman yasa Adewale ya tura  masa su,  a cewarsa shima zai turawa matarsa domin taga irin style din da yake so  tayi dinga yi masa idan ya dawo gari.

Adewale abun nema ya samu a take ya tura masa kala-kala wanda har sai ya rintse ido gurin kallon wasu daga ciki, don dai ma yana da kok'arin danne sha'awarsa amma da anyi katari da mara hakuri ganin sticks din zai sanya shi  aikata aiki mara kyau.

Yana tura mata ya sauka daga layin ya dauki daya wayar tasa  kai tsaye what'sApp din ya shiga tana online har yanzu.

Sai kawai yay mata magana.

_"Me kike a online?  karfe goma sha biyu da rabi."_

Ganin shigowar sakonshi yasa gabanta mugun faduwa!.

Koda ta duba  sai ta kasa magana,  baki da jikinta gabadaya sun mutu in banda faduwa babu abunda gabanta keyi   a dabarbace ta  kashe wayar ta kwanta lamo kan gado ganin sticks din ya sanya  ruwan ni'imar da ya saba zuba a jikinta yin 'karfi, gabadaya pant din ya jike ta dinga takure jikinta guri guda yanayin yana sake shiga jikinta sakamakon tashi da tsigar jikinta  keyi nipples dinta basu ta bayi mata 'kai'kaiyi irin na ranar ba.

Haka ta kasance cikin mawuyacin hali har asubah bata rintsa ba sakamakon ciwo da cikinta ke mata.

Da 'kyar tayi sallah ta koma ta kwanta lamo kan daddumar ..........dole taja masa kunne kan cewa kada ya sake turo mata da hotonan iskanci.

Misalin bakawai da rabi  na safe,  Baraka wato daya daga cikin hadimanta tayi knocking din kofar dakin.

Ta mike zaune da kyar da fadin." Waye."?

Cikin girmamawa tace." Baraka ce ranki shi dade."

Sai da ta dauki kusan minti biyar sannan ta tashi taje ta bude mata kofar.

Tana shigowa ta zube gwiwa biyu tana gaisheta.

Da kyar ta amsa ta nemi saman sofa ta zauna yanayinta kadai shi zai nuna maka cewa akawai abinda ke damunta.

Ta kalleta da kulawa tace."Ranki ya dade ko bakya jin dadi  ne? domin naga alamun haka."

Girgixa mata kai tayi da fadin."Lafiya ta lau  ina Marakissiya."? tana nufin 'yar uwarta da suka zo tare.

Da sauri tace."Tana kicin domin had'a miki abin kari."

Tace."Okey ki hada min ruwan wanka, sannan ki shirya min kayana cikin wardrobe ki ajiye komai a muhallinsa."

Cike da bin umarni ta amsa da "an gama Gimbiya." Mikewa tayi da sauri ta kama hanyar toilet

din sai ta dakatar da ita da fadin." Ruwan da d'umi sosai zaki had'a min kinji ko."

Ta amsa da "To ranki ya dade." Toilet din ta nufa cikin bin umarni.

Bayan ta hada ruwan ta fito sheda mata sannan ta fara sauke akwatinan kayan domin gabatar da aikinta na gaba.

Ta dauki kusan minti goma a zaune kafin ta yunkura ta tashi domin shirin wankan, kira ya shigo wayarta dake can kan daddumar da tayi sallah.

Kafin ma ta bata umarni taje ta dauko mata wayar, ta karba a yatsine tana dubawa.

*BA 'KYAUE* sunan dake yawo kan fuskar wayar kenan.

Tsaki taja da fadin." Da sassafe ya kira waya kamar wanda yake bin bashi.....Daf da zata tsinke ta daga tasa a kunne.

A maimakon tai masa sallama sai kawai ta sauke masa ajiyar zuciya a kunne, tai shuru da bakinta.

Shi yay mata sallamar ta amsa kamar bata so, yace."Kin tashi lafiya ya kwanan ba'kunta."?

A takaice tace."Alhamdulillh." Ya dan ja fasali kafin yace."Jiya na gan ki a online misalin daya na dare ke da waye."? Cikin sigar zargi da tuhuma yake mata tambayar.

Gabadaya duk sai ta daburce! tana so ta tonawa kanta asiri........."Wac....Wace irin tambaya ce wannan."?

Yace."Alamu sun nuna baki da gaskiya ga yanayin yanda kike magana a daburce! okey duk wani abu da za kiyi ina ji a jikina domin bani kadai bane akwai masu sheda min halin da kike ciki saboda haka ki shirya dawowata sati biyu masu zuwa."

Da kyar ta iya saisaita muryarta amma inaa! sautin muryarta rawa yake yaki saisaituwa duk ta tsure jin yace bashi kadai bane dama tun haduwarsu a daji ya ta'ba fada mata cewa yana da aljanu tana jin tsoron kada su sheda masa halin da take ciki, Ta daure da 'kyar tace." Bana neman tashin hankali ko wata 'bakar magana zargin da kake min ba zan ha naka ba ka cigaba sannan duk sharrin da aljanunka za suyi min sun jima ba suyi ba, dai kai dasu duk baku dame ni ba." Tana gama maganarta ta kashe wayarta ba ta jira amsarsa ba.

Shi kam dariya ma ta bashi ya tsaya ya dara yana jin dadin yanda game din yake tafiya a tsakaninsu, Hamra'u ya kira suka gaisa ganin zata jashi da hira alhalin fita zai yi yasa a tausashe yace." Kanwata yi hakuri yanzu ba lokacin hira bane lokacin aiki ne idan na dawo na

samu nutsuwa zan kira ki muyi hirar soyayya, yanzu ki bani Uwale idan tana kusa mu gaisa domin na kira wayarta bata shiga ba."

Taji ciwon hakan a cikin ranta amma sai ta danne a sanyaye tace" Bari na kai mata wayar tana kicin.?

Cikin mamaki yace."Kicin kuma me takeyi? Hamra'u keyi menene amfaninki."?

Da sauri tace."Aa nima ba laifina bane domin babu yanda banyi da ita ba akan ta zauna ta huta ni zanyi mana komai kamar yanda na saba tace ita lallai sai ta shiga kicin da kanta tayi wa amaryarka girki."

Ya dinga girgiza kai yana mamakin rigima irinta kakar tasa, yace." Yanzu je ki kai mata wayar za muyi magana."

Ta amsa da "to" kafin ta je ta kai mata wayar.

Tana kicin taa dage sai soya funkaso take gefe guda kuma had'addiyar miyar taushe ce wacce taji nama da gyada da alayyahu sai turiri take tana tayar da kamshi mai dadi.

Tace."Uwale yayana yana son magana dake."

Da farin ciki ta karbi wayar tasa a kunnuwanta da fadin." UMARU ina kwana."?

Ya amsa da "Lafiya lou Uwale kun tashi lafiya ya kuma hidima da jama'a."?

Tana 'yar dariya tace." Alhamdulillhi an yi taro lafiya jama'a kowa ya koma gidansa lafiya "

Yace."To alhamdulillhi haka akeso nima insha Allahu sati biyu masu zuwa na kammala komai na dawo gida."

Tace."Alhamdullhi, Allah abin godiya UMARU Allah ya dawo da kai lafiya ya kuma cigaba da baka nasara akan duk abunda kasa a gaba."

Ya amsa da "Ameen ya Allah." Ya dora da fadin." Yanzu Hamra'u take sheda min cewa kina kicin kina aiki Uwale me yasa ba zaki zauna ki huta ba sai kin wahalar da kanki Hamra'un za tayi duk abinda ya dace."

Tace."Hakane maganarka UMARU bahaushe yace YABA KYAUTA TUKWICI yarinyar nan 'yar babban gida ce wannan shine dalilin da yasa nake dawainiya da ita ba wai don naga gazawar ita Hamra'un ba."

Yace."Duk da haka dai ki samawa kanki lafiya domin ba na so kina aikin wahala saboda

shekaru sun ja miki, idan ya kama na dauko masu hidima a gidana ina da ikon yin hakan, domin itama Hamra'un ba ita take da alhakin haka ba tunda dai ba auranta nake ba."

Tace." To yanzu dai nayi laifi kenan don na nuna kulawa a kan matarka."? Ya girgiza kai da fadin." Ba kiyi laifi ba Uwale cewa nayi ki zauna ki huta ita Hamra'u ta cigaba da aikinta kafin na dawo gari."

Tace."Ai shikkenan tunda kai baka san gwaninta ba sai anjima." Sallama tayi masa ta mikawa Hamra'u wayar tana mita akan abunda yay mata.

Yace." Hamra'u bata wayar da sauran magana dani da ita.

K'in kar'ba tayi yana jinta tana fadin." Oho!oho! ai ka gama magana UMARU har da zan nuna kulawa kan matarka ka gwasale ni."

'Yar dariya yay ya daga murya yanda za taji sosai yace."
Yanzu dai mu bar wannan maganar haka Uwale kina ji na ko."?

Shuru tai masa ta cigaba da soya funkasonta.....Ya cigaba da cewa." Wannan kayan abincin da aka jibge a store ba na bukatar na dawo na samesu, ki tara 'yan uwa da abokanan arziki da kuma yara na ina nufin su Alba kenan duk ki raba musu, ni a bar min kadan sun isa."

Tace."Kana da hurumin hakan amma sai an shedawa ita GIMBIYAR domin itama tana da hakki."

Ya jima yana mamakin maganar kafin yace." To shikkenan ki sheda mata cewa Umarni na ne nace rabawa mabukata kayan masarufin da tazo dasu sannan kuma nagode da hidima."

Tace." UMARU ba haka sharad'in kayan gara suke ba, kana da hakki tana da hakki, saboda haka ni sai naji hukuncin da ta yanke idan bakinku yazo daya shikkenan sai ayi yanda kace."

Takaici ya ishe shi, kawai ya kashe wayarsa ba tare da yayi mata sallama. aljihu yasa wayar, ya janyo takalmansa ya fara kokarin sanya wa a kafafuwansa dake cikin safa, yana ganin idan an jima kadan, ya samu sukuni zai kira yarinyar ya sheda mata hukuncin da ya yanke, bawai don baya bukatar kayan masarufin ba, kawai dai yana so ya tsira da mutuncinsa domin ganin tsarin yarinyar watarana zata iya yi masa gori akan wani abu daya dangance ta.

*SAI RANAR MONDAY ZA MU CIGABA DA IKON ALLAH🙏🏻 NA 'DAUKI HUTUN KWANA BIYU A CIKIN SATI DAYA, INA GODIYA A GARE KU🙏🏻*

*Kika futar min da littafi keda Allah!  ki ka karanta baki biya ba kema keda Allah!*

*#500via.....0542382124.....Binta umar gtbabk, idan kati zaki turo  kiyi min magana ta WhatsApp da wannan number.... 07084653262.....BINTA UMAR ABBALE*
[2/6, 11:42 PM] Matar Malam: *G-J-S-U-R*
*57&58*
'Daure da towel mai dan girma wanda ya sauko mata har kasan gwiwa  ta fito daga toilet din har yanzu akwai sauran damuwar a tattare da ita sai kace wacce ta jima tana kuka   idonta yayi wani ja  bayan 'kan'kancewar da sukayi  wannan shine dalilin da ya sanya  Baraka baiwar ta dake aikin jera mata  tufafinta a wardrobe ta fara lallaminta saboda  duk wani  abunda yake faruwa suna da labarinsa.

 Rarrashinta take sosai tana kara  'kwantar mata da hankali tare da bata shawarwari masu kyau wanda idan ta dauk'esu to tabbas  za taci riba anan a gaba.

A 'kalla Baraka za ta iya shekaru talatin da biyu a duniya,  ta girmeta da wasu shekarun shiyasa take da sinkaye da hangen nesa, kuma dai itama haka kawai take sha'awar uwar dakin nata tayi zaman aure kamar yanda sauran 'yan uwanta suke zaune a dakinsu lafiya,  sau daya ta ta'ba ganin mijin nata a zahiri amma duk iya bin k'wa'kwkwafin ta bata hango wani nakasu a tattare dashi ba, namiji ne na nunawa sa'a irin mazan da suke da wahalar samu,  'yan mata da yawa ire-iren ta gasu nan  birjik duk a zaune babu mijin aure, wannan dalilin ne yasa take mamakin wasu 'yan matan idan dadi yayi musu yawa suke tsula tsiya iri-iri,   ita dai  kam ba taga abun gudu a cikin auran mutumin ba domin ya tara duk abunda ake da bukata.

Jiki a sanyaye ta zauna kujerar mudubi tana dan goge  guntun hawayen da suka sauka a fuskarta, maganganun Baraka sun kashe mata jiki mutuka,  ta rasa mai mutane suke hango mata a tattare da zamanta da mutumin nan,  duk wanda zai bude baki sai yace mata shine alkairinta,  ba ta'ba gani ko jin wanda ya soki al'amarin ba, sai mutum daya wato Sakina kawarta amma tun daga kan family nata har zuwa kan bayin dake cikin masarautarsu dukkaninsu farin ciki da al'amarin suke,  ita da Sakina su kadai ne suke nuna adawarsu a fili,  tana ganin dai mutumin bai zauna haka ba sai da ya nemi jama'a domin gabadaya ya siye zuciyoyin duk wanda ya shafe ta.

Tana shirya jikinta tana auna maganganun Baraka a zuciyarta da kuma tunanin yanda za tayi zaman aure da mutumin bayan har yanzu ya kasa fuskantar alkibula ma'ana ya kasa fahintar abunda take so da wanda ba ta so.

Tazo ta gurfana a gabanta da fadin." Ranki ya dade na kammala komai  akwai bukatar wani abu."?

Ta kalleta cikin rashin walwala tace." Babu bukatar komai a yanzu, sai ko zuwa anjima kina jina ko."?

Da sauri tace."Eh ranka ina jinki."

Tace."Kada na kuskura naji kin sake yi mib magana makamanciyar wannan, ki kiyaye ki kuma zauna a matsayinki."

Baraka jikinta yayi sanyi cikin bin umarni tace."Allah ya huci zuciyar Gimbiyar mata insha Allah zan kiyaye ba zan kuma."

Ba tare da tace komai ba ta nuna mata hanya da hannu, ta mike cikin rashin kuzari ta kama hanyar fita tana zancan zucci, itama mantawa tayi da halin uwar dakin nata ta san ta da gwale mutum, amma meye laifinta anan don ta nuna mata hanyar gaskiya, shikkenan ai daga yau zata kiyaye harshen ta ko don ta tsira da girma da mutuncinta.

Kacibus sukayi da Markisiyya ta gama shirya daining zata shiga ta sheda mata.

Ta kalleta da fadin." Ya naga kin fito da jiki a sabule."?

Girgiza kai tayi kafin tace." Marakissiya kin san halin mutuniyar sai ana kai zuciya nesa shiyasa kwata-kwata ban so dani a cikin wannan tafiyar ba.

Tace."Nima haka wallahi kin san bamu da ikon da zamu nuna rashin yardar mu akan haka to kinga dole muyi hakuri kuma mu kiyaye zama da ita."

Tace." K'warai hakane maganarki ki shiga ki sheda mata kin kammala ina jiran ki anan."

Tace."To shikkenan jira ni na fito.

Zubewa tayi kasan gwiwa ta gaisheta kafin ta sheda mata cewa ta kammala shirya gurin cin abinci.

Ta kalleta da fadin." Me ki kayi.'?

Ta shiga lissafo mata abinci har kala uku.

Sosai ta rufe ta da fad'a da fadin taje ta kwashe kayan abincinta bata bukatar cin abinci mai nauyi da safe, tayi maza ta soya mata k'wai da indomee da kuma ruwan tea, Cike da bin umarni ta amsa kafin tai saurin fita daga dakin..

Ita da Barakan suka fita suna munufurcinta da irin munanan halayen ta marasa kyau.

Bayan fitarsu da 'yan mintina Uwale ta shiga hannunta rike da kwando wanda yake dauke da kayan abinci.

Ta kai tsayin minti goma tana sallama, ta naji ba ta amsa ba ballanatana ta fito.

Ta jima a tsaye tana shawarwari da zuciyarta kafin ta yanke shawarar shiga uwar dakin jikinta yana bata cewar ko babu lafiya.

Tana tura kofar dakin kawai ta sameta a hakimce a kan kujera tana latsa wayarta, kamar bata so ta amsa sallamar still hankalinta gabadaya yana kan waya bata dago ta kalleta ba, ballanatana taga da me ta shigo.

Uwale ta samu gefe ta ajiye kwandon kayan abincin da 'yar fara'a ta tattare da ita tace." Yarinyar arziki ina fata kin wayi gari lafiya ya kwanan bakunta kuma."?

Shuru tay mata still dai hankalinta na kan wayarta.

Tace." Ga abinci nan nayi miki da kaina na shiga kicin, funkaso ne da miyar taushe da kuma kunun gyada da 'kosai nasan zakiyi sha'awar ci, bayan haka kuma dazu UMARU yayi waya yake cewa wannan kayan masarufin da ki kazo dashi da kuma atampopin duk yace a bayar dasu ga mabukata shine nace lallai sai naji hukuncin da ki ka yanke."

Kamar ba taso ta kalleta kafin tace." Bani da damuwa da duk abunda kukayi da kayan, na kune duk wanda kuke so zaku bawa bani da matsala."

Tace." To masha Allah mungode sosai Gimbiyar mata ga abinci nan a jiye duk sanda kika kammala sai kici kada ki zauna da yunwa."

Ta kalleta a karo na biyu tana yaba k'okarinta, koda yake dole tayi duk wani kokari a kanta tunda tana kwad'ayin ta zauna da jikanta.

Girgiza kai tayi kamar tace mata fita da kayan ki bana bukata, sai dai kawai tayi mata shuru har ta fita daga dakin ba tanka mata ba ballanatana tayi mata godiya.

Asp ne ya kira ta suka gaisa cikin sakewa yana tsokanarta tana amsawa sama-sama, kafin yace" bari na baki kawarki ku gaisa ko."?

Tace" Bata wayar daman yanzu nake tunanin kiranta."

Yace." Kin dai yar  da Madam bayan da tsohowar zuma ake magani baki kyauta ba."

Aunty Zeey dake zaune a kusa dashi ta dinga zabga masa harara.

Ita ya ambaci sunan matar ma bata so saboda tsananin kishinta.

Daga  daya bangaran Zinat din tace." Aa ba haka bane wallahi Mommy uwa ce a gareni kuma har yanzu ban mance alkairinta ba, sannan ka tambayeta ai muna waya sa'i da lokaci muna gaisawa har da Nabila."

Yaji dadin hakan a ranshi yace." Masha Allah naji dadin haka ki dauka cewa da Madam da ita Zainab din duk 'yan uwanki ne.''

Tace."Dama ai haka na daukesu a cikin    raina.''

Ya mikewa Zeey wayar ta kar'ba tana jin haushinsa,  da ya lura da hakan sai kawai yayi murmushi yana girgixa kansa, ya rasa mai yasa ta zafafa akan al'amarin uwargidanta.

Ba suyi wata hirar kirki ba a tsakaninsu, dalili Asp din yana gurin shiyasa Aunty Zeey din ta katse hirar da fadin.'' Zan kira ki an jima idan na sallami Oga zai tafi gurin aiki.''

Tace."Okey to babu damuwa."  Sallama sukai kafin kowa ya kashe wayarsa.

Da ido kawai ta kalli funkason da miyarsa ta tabbatar da cewa zai yi dadi,  duk da cewa bata cin abinci mai nauyi da safe, ganin funkason shar da miyarsa da take tashin kamshi yasa yawun bakinta tsinkewa,  ta bude fulas din kunun gyadan shima yay kyau fari tas dashi sai k'amshi yake,    dama can tana son kunun gyada da k'osai saboda haka ta kansu ta fara,  tana kurbar kunun tana had'awa da kosan, zuciyarta cike da mamakin yanda tsohowar ta iya girki dad'i gaske,   wani irin gardin dadi kunun keyi mata, kamar kunnanta ya tsinke.

Saboda tasha kunun da yawa funkason biyu kacal ta ci, ba don ta hak'ura ba, sai an jima za ta zauna taci a tsanake idan cikinta ya samu sassauci.

Koda Marakisiyya ta shigo ta sheda mata cewa ta kammala aikinta, sai kawai  tace taje dashi suci  bata bukata har da  ta nuna mata kwandon abinci Uwale  da fadin." Ita   ta samu wani wanda ya gamsar da ita.

Marakisiyya taji ciwon abunda tai mata, amma ba yanda za tayi haka tayi godiya tabi umarni ta fita ta kwashe tarin abincin da tayi ha'kilon dafawa  ita da Baraka sukaci wanda zasu  iya kafin su fita da sauran su kaiwa 'yan uwansu maza da suka zo tare.

 Ta kira wayar Sakina ya kai sau biyar amma  sai ace da ita busy,  tsaki taja tare da mi'kewa tsaye, falo ta nufa gabadaya babu kuzari a tattare da ita, dole tana bukatar wanda zai dan d'ebe mata kewa, amma bata tsammanin sauraran boyyayan masoyin nata a kusa duba da irin abinda yay aikata mata saboda kawai ya samu  fuska a gurinta,  dole ne ta nuna masa kuskuransa.

Aikuwa tana tsaka da wannan tunanin kiran sa ya shigo wayarta,  tana kallo har wayar ta katse bata daga ba.

Ya kira ya kai sau biyar bata dauka ba.

Text ya tura mata cewa ta daga wayarsa yana so yayi magana da ita.

Ta mayar masa da amsa kamar haka.

_" Saboda kawai ka samu fuska shine zaka turo min hotonan banza ko an fada cewa ni din 'yar iska ce."?_

Murmushi yay lokacin da ya karanta text din ya mayar mata da amsa kamar haka.

_"My love kiyi hakuri ba zan sake ba tunda bakya so amma ki daga waya ta ina bukatar jin muryarki."_

Share shi tayi bata bashi amsa ba, koda ya sake kira ma tana kallon wayar taki dagawa.

Yaji dadin hakan a ranshi  amma duk da haka ba zai kyaleta ba zai cigaba da gwadata domin ya tabbatar da nagartar ta.

****

Sai bayan isha'i ya samu kansa dan gabadaya yau a tsaye suka wuni, yayi wanka ya fito cikin k'ananun kaya t- shart da 3Qutar masu haske kai tsaye falo ya nufa ya samu Adewale yana kallo ga plate din abinci nan a gabansa.

Kusa dashi ya zauna yana kiran sunan Allah, hannu yasa ya dafe kanshi da fadin." Ba haushe

yace Aski idan yazo gaban goshi yafi zafi Adewale kwana Biyu nan wallahi a gajiye nake gashi bana samun bacci isasshe."

Cokali cike da abinci ya kai bakinsa yana taunawa yace." Oga aikin nan namu ai sai mai juriya akwai tarin kalubale wanda ba kowa ne zai gane ba sai wanda ya san ya al'amarin yake, ni kaina na matsu na koma gida domin dukan yayi yawa ban ta'ba kwana uku babu sex ba sai da nazo garin nan, shiyasa wani sa'in nake fita na rage zafi."

Yana girgiza kansa yace."Adewale baka da magana sai ta sex kai kenan kalle-kallen blue film ko gajiya ba kayi wallahi ka kiyaye kuma kai hattara kada garin son zuciyarka kaje ka dauko ciwo neman mata bashi da fa'idah."

Shiru yay na minti biyu kafin yace." Oga ina kiyayewa fa bana yarda na kwanta da mace ba tare da kariya ba, bani da juriya akan wannan al'amarin Oga haka Allah ya hallice ni, kai kam ai ina ganin k'okarin ka don ban ta'ba ganinka da wata mace ba."

Yace." Kariyar banza, ai duk wayonku ba zaku hana Allah zartar da ikonsa ba, wallahi ka kiyaye domin inganta rayuwarka data 'ya'yanka."

Yana 'yar dariya yace." Oga kullum aka zauna da kai sai ka kashewa mutum jiki da nasiha, duniyar nan fa ita kenan to me zai sa mutum ba zai ji dadinsa ba."

Ya kai hannu ya janyo plate din abinci dake rufe ya bude da fadin." Kayi nisa Adewale sai dai kawai na taya ka da adduar shiriya."

Ya mike tsaye yana kyalkyala dariya da fadin." Yanda yau muka yini a tsaye da zaka bani hadin kai da na kawo maka wacce zaka sauke gajiyarka."

Shuru yay masa be iya ce masa komai ba, domin al'amarin mutumin yana nema yafi k'arfinsa.

Ya cigaba da subararsa yana jinsa uffan bece masa ba, abincinsa kawai yake ci yana nema masa shiriya a gurin Allah.

Gajiya yay da surutun ya kama hanya ya fita da niyyar zuwa ya samu wacce zai sauke gajiyarsa a kanta.

A nutse ya kammala cin abincin ya yagi tissue ya goge bakinsa, hamdala yay ga Allah, kafin ya kishingida kan kujerar ya dauki wayarsa yana dubawa.

Ya kai mintina goma yana duba wayar kafin ya lalubi number abokiyar rigimar tashi.

Daf da zata katse ta daga wayar, wannan karon ma a maimakon tai masa  sallama sai kawai ta shiga  sauke masa  ajiyar zuciya a kunne.

Lumshe idonsa yay ya janye wayar daga kunnansa yana jin wani irin yanayi na shiga  jikinsa, ya ci ya 'koshi ga gajiya jikinsa yayi  tu'bus!  ta bakin Adewale san samu ya samu wacce zai sauke gajiyarsa,  cikin wannan yanayin ita kuma tazo tana masa numfarfashi a kunne sai kace wacce take cikin wani yanayi.

Jin shuru bece komai ba yasa ta cire wayar  tana dubawa, har yanzu yana kan layin bai kashe ba.

Zum'bura baki tayi ta ya mutse fuska da fadin." Ina jinka ka kira waya kuma kayi shuru"

Gyaran murya yayi ya saisaita yanayin sa da fadin." Ya kike ina fatan kin wuni lafiya."?

A takaice tace." Lafiya."

Yace." Masha Allah haka ake so menene labari."?

Tai masa banza tana jin kamar ta kashe wayarta.

Yace." Baki da labari me dadi wanda zaki bani."?

"Umm." tace tana jin wani irin haushinsa a zuciyarta.

Yace." Okey d'azu da safe munyi waya da Uwale ina fatan ta sheda miki hukuncin dana yanke akan wannan kayan garan da ki kazo dashi."

Tace." To ni me ya dame ni da wannan, al'adah ce ta masarauta cewa duk yarinyar da za'ayi wa aure sai an had'a da kayan masarufi da turaman atamfofi da sauransu,  kai akayi wa hidima da sauran family naka duk yanda kukayi dai-dai ne."

Yace." Eh na fahimta bana bukata ne shiyasa nace a bayar dasu kafin na dawo Uwalen take sheda min cewa lallai sai an fada miki kin yanke hukuncii tukkuna."

Tace." Kai har kafi 'karfin wani abu kenan."?

Yace." Ban fi k'arfi ba kawai bana bukata ne."

Ranta yay masifar baci tace." Nawa kake dashi? me ka ajiye a banki? shin yaushe ma ka zama

mutum! ka samu sutturar sanyawa da har za ayi maka kyauta kace baka so, shin wanene kai a cikin mutane da har zaka nuna cewa kai kafi karfin wani abu."!? Cikin daga murya take maganar."

Yace." A'm human being ni mutum ne kamar kowa nace bana bukata idan da akwai wanda ya isa ya sauya min ra'ayi ina jiran sa."

Taja wani mugun tsaki irin wanda ta san baya so a kufule! tace." Nonsense kawai." Kashe wayarta tayi zuciyarta na wani irin turiri, sosai taji ciwon abinda yayi, shi din har waye da mahaifinta zai masa kyauta ya k'yama ta, yaushe har ya zama mutum yayi arziki gami da sutturar sanyawa da har zai nunawa duniya cewa shi yafi karfin a taimaka masa, wannan abun yayi mata ciwo sosai! a ganinta hakan kamar tozarci ne....

*Kika futar min da littafi keda Allah! ki ka karanta baki biya ba kema keda Allah!*

*#500via.....0542382124.....Binta umar gtbabk, idan kati zaki turo kiyi min magana ta WhatsApp da wannan number.... 07084653262.....BINTA UMAR ABBALE*
[2/8, 9:24 AM] Matar Malam: *59&60*
Da tsananin bacin rai ya kwana ya kuma tashi dashi, a cikin ranshi yana raya irin tsauraran matakan da zai dauka akan yarinyar mutukar ya koma gidan tazo masa hauka da rashin hankali makamancin wanda take masa a yanzu, wanda yayi imani da cewa don baya kusa da ita ne amma da ba don haka ba da kudi a kace ta zage shi ko taci masa fuska ba zata iya ba.

Yana tsaka da shiryawa Hamra'u ta kira shi a waya. beyi a kasa a gwiwa ba ya d'auka tare da gyaran murya kafin ya ambaci sunanta." Hamra'u."

Ta amsa da 'yar dariya a tare da ita tace." amma bana son wannan sunan nafi bukatar da ka kira ni da my love din ka kamar yanda ka saba kira na."

Murmushi yayi tare da kokarin kawar da damuwarsa yace." Ashe nayi laifi don na kira ki da sunanki na hakika okey to My love dina haka kike so ko."?

Ta shiga kyalkyala dariya farin ciki duk ya cika mata zuciyarta tace."Ina son wannan sunan a bakin ka yaya na."?

Murmushi kawai yayi, yana k'ok'arin d'aura takalminsa tace." Na san dai yanzu kana shirin fita ko."?

Yace." K'warai kuwa kiran wayarki ne ya dakatar dani, ina fata dai kun tashi lafiya? idan Uwale

na kusa bani ita mu gaisa."

Tace." Yau ma tana kicin tana aiki."

Shuru yayi ransa ya b'aci sosai, shin wai mai yasa Uwale ba zata zauna ta hutar da kanta ba.

Yace." Kema kina da laifi Hamra'u me yasa ba zaki kar'be ta ba."

Tace."Wallahi babu yanda ban yi da ita ba akan cewa ta bari amma taki amma dai bari naje kicin din na same ta."

Yace." Yawwa kiyi min wannan k'okarin kafin na dawo kema zaki zauna ki huta tunda baki da hakki akan hakan na ma fasa daukar masu aiki, ita matar gidan da kanta zata shiga kicin tayi ayyukanta, babu ruwana da wani mulkinta."

Farin ciki kamar ya kasheta tace." To shikkenan Yaya na Allah ya dawo da kai lafiya."

Ya amsa da "Ameen kafin ya kashe wayar, ya cigaba da shiryawa.

To da kyar dai Hamra'u ta shawo kan Uwale ta fita daga kicin din, ita kuma ta d'ora a inda ta tsaya, amma inaa! sai da hannu ya bambamta girkin tsaffi ya fita daban.

Ta kammala ta tsaf ta shirya wanda za'a akai wa Zinat din a kwando ta fito ta sheda mata cewa ga abincin can a kicin.

Tace." Ai sai ki 'karasa ladan ki, ina nufin ki d'auka abincin ki kai mata, dama naga baki ta'ba shiga kun gaisa da juna ba."

Tace." Uwale nifa bana san shiga sabgar matar nan tunda naga bata da kirki wallahi yanzu ma kawai umarnin yaya na ne, amma ba don haka ba wallahi ba zanyi mata bauta ba, kuma kina maganar na shiga gurinta domin mu gaisa ai ita ya kamata ta fara zuwa inda muke tunda mu ta zo ta samu a gidan."

Tace."Hamra'u duk na gane inda kika dosa, kada kice zaki fito da kishin ki a fili har yarinyar nan ta gane akwai wata ala'ka a tsakaninki da mijinta, ina so kibi komai a sannu a hankali."

Cike da jin haushin maganarta tace." To ni ina ruwa na don ta fahimci da akwai soyayya a tsakanina da mijinta, dama abunda nake so ta sani kenan cewa akwai alkawarin aure a tsakaninmu, bayan haka kuma Uwale naga kamar kin fi k'aunar ta a kaina, to bari na tuna miki idan kin manta nice taki kafin ki nuna kulawa da kauna akan wata a kaina ya kamata ki nuna."

Ta ri'ke baki da mamakin maganganunta tace." Hamra'u rashin kunya zaki min daga fada miki gaskiya shine zaki gaya min magana."

Fashewa tayi da kuka da fadin." A'a ni ba nufi na kenan ba, kawai dai naga abunda kike bai dace ba shiyasa nai miki magana domin ki gyara dan gaskiya ba zan boye miki ba ina jin takaicin halin ko'in kulan da kike nuna min wallahi da kin so da tuni UMARU ya aure ni amma kin mayar da abun wasan yara." Tana kuka sosai take maganar.

Uwalen hankalinta ya tashi domin tunda take da yarinyar bata ta'ba yi mata rashin kunya irin na yau ba, kuma tabbas ta sheda cewa yarinyar 'yar halak ce."

Tace."Kiyi hakuri ki daina kukan hakan, idan da wacce nafiso Umaru ya aura to kece ta farko, sai dai kuma kin san komai nufi ne na Allah, duk yanda muka so ki auri UMARU idan Allah bai nufa babu yanda za muyi, wannan auran kuma da yayi daga Allah yake domin shima da bakinsa ya fada cewar kece za'bin sa, sai gashi kuma Allah ya kawo masa wata bayan ke, bamu san alkairin da yake tattare da al'amarin ba, sannan kuma idan kin kwantar da hankalinki kema idan da rabo zai aureki tunda yana sonki, amma ki daina fito da kishinki a fili akan wannan al'amarin.'

Duk cikin maganganun Uwale babu na son zuciya gaskiya ce amma ita kuma sai ta kasa fahintar hakan, ta juya al'amarin wata siga daban, ta kuma 'kullaci Uwalan a cikin ranta a ganinta kamar itace bata so UMAR din ya aureta.

Hawayen fuskarta ta goge ta nufi dakinta mayafi ta yafo a jikinta, kicin din ta nufa ta dauki kwandon abincin kai tsaye sashen Zinat d'in ta nufa.

Ta same ta zaune a falo cikin shiga ta alfarma, Alkyabba 'yar gasken, gold yaji a ko'ina har a yatsun kafa, falon ban da k'amshi na mussaman babu abunda yake, kallo daya tayi mata taji gwiwarta tai sanyi, Gimbiyar tana da wani irin k'warjini na mussaman wanda Allah ya huwace mata.

Jin motsi yasa ta dago kanta tana kallon bakin kofar, lokacin ita Hamra'un ta juya tana rufe kofa, bata dauke idonta ba har sai da ta juyo suka had'a ido.....Wani irin kallo ta kai mata wanda gabadaya ya kashe mata jiki, daman abinda ta guda kenan.

Ta daure tayi mata sallama tare da k'arasawa kusa da ita da kwandon abincin a hannunta.

"Auntyna barka da asubah fatan kin tashi lafiya."? Cikin nutsuwa take gaisheta.

Kafin ta amsa sai da ta mula tukkuna!

Ta d'an janyo kwandon abincin da fadin." Ga kayan kari kummalo nan Uwale tace a kawo miki."

A d'age tace." Tsakanin ke da ita wacece tayi girkin."?

Kai tsaye tace." Ni ce nayi saboda Yayana ya bada Umarnin hakan cewa ita Uwalan ta zauna ta huta, ni na gabatar da komai kafin ya dawo."

Ta jima tana kallonta gami da auna maganarta tace." Shin kece kika fada masa cewa kakarsa tana min hidima."?

Shuru tayi ba tace komai ba.

Ta ta'be bakinta da fadin." Okey shurun ki ya bani amsa, ki tashi ki bani guri tare da wannan tarkacan k'azantar da ki ka shigo min dashi bana bukata."

Ba tace mata komai ba, ta yun'kura ta tashi tsaye, kwandon abincin ta d'auka ta kama hanyar fita, zuciyarta cike da takaici da haushinta.

Kallon banza tabi dashi, cikin zuciyarta tana raya wasu abubuwa akan yarinyar, tabbas akwai alamun munafurci a tare da ita.

Gabad'aya ta riga ta saki jiki tana jiran abinci mai dadi da gamsarwa irin na jiya, wannan shine dalilin da yasa koda Marakissiya ta tambayata abunda take bukata ta dakatar da ita da cewar taje kawai tayi musu nasu, ita tana jiran wanda za'a kawo mata daga cikin gidan, sai kuma yanzu taga a kasin haka, tsaki taja mai tsayi, sam bata tsammanin zata iya cin abincin yarinyar domin bata yarda da tsabtarta ta ba.

Shigowar Uwale ne ya katse tunaninta, wannan karon a d'an sake ta amsa sallamarta, bata kuma dauke idon ta ba har sai da ta k'araso inda take zaune.

Cikin damuwa tace." Zinatu me ya faru ne? Hamra'u ta kawo miki abinci kin kore ta dashi."

Numfashi ta sauke kafin tace." Babu komai kawai bana bukatar nata, nafi bukatar naki domin wanda ki kawo min jiya yay min dadi sosai."

Ta 'bangale baki tana dariyar farin ciki tace."Shine dalili kenan to kada ki damu idan kinfi bukatar nawa nayi miki alkawarin yi miki duk irin wanda kike so."

Murmushi tayi da fadin." Nagode sosai, me zaki min yanzu? amma dai ina bukatar kunun gyada irin na jiya."

Tace." To kada ki damu yanzu zan je na dama miki bayan shi sai me kuma."?

Kallonta tayi cikin zuciyarta tana yaba kokarinta, a rayuwarta tana son mai sonta, lokaci guda taji tsohowar ta kwanta mata a rai."

A sake tace." duk abunda ki kayi ina bukata, Ina yaba kokarin ki sosai koda yake dama girkin tsaffi akwai dadi da gamsarwa."

Ta kyalkyala dariya da fadin." 'Kwarai haka maganarki take, ai mutanan da bamu da 'kyiwa da ganda muna zama mu gyara abinci yanda zai gamsar, mijinki ma Umaru haka yake min irin wannan sambatun."

Murmushi kawai tayi, bata iya cewa komai ba, har Uwalen ta fita daga falon, Ta girgiza kai da fadin." Kakar sa mai kyawun hali, shi kam halinsa daban da sauran mutane.

Ganin Uwalan ta shigo cikin farin ciki da walwala ya sanya ta mamaki, ta bita da kallo a lokacin da ta kama hanyar kicin, sai ta shiga nazari da tunanin abinda ya sanyata walwala da farin ciki irin haka, dalili duk lokacin da zata shiga sashen Gimbiyar to babu shakka zata fito da bacin rai amma yau sai aka samu sauyi.

Tana nan zaune tana saka wasikar jaki tsayin mintina arba'in Uwale ta fito daga kicin ta kammala komai hannunta rike da kwandon abincin.

Ta dinga yi mata kallon mamaki! kafin ta bude baki da niyyar magana Uwalan ta riga ta da fadin." Hamra'u kada kiyi wa al'amarin nan mummunan fahinta, domin ni dake da Zinatu duk daya na dauke ku a zuciyata, bayan na shiga gurinta take sheda min cewa tafi bukatar ni nayi mata abinda za taci saboda taji dadin wanda nayi mata jiya, don haka kada ki sanya a ranki cewa domin ta tozartaki ta 'kyamaci abincinki."

Kasa magana tayi tsabar bacin rai da yanda zuciyarta take tururin zafi, zuwan gimbiyar gidan yana barazana da rayuwarta domin abubuwan da Uwale take mata zasu iya sanyawa zuciyarta ta buga......Tana can tana tunani Uwalen ta fita motsin kofa ne ya dawo da ita nutsuwarta.

Ajiyar zuciya mai zafi ta sauke kafin ta mike ta nufi dakinta.

Tana shiga ta zauna gefan gado tare da daukar wayarta, kai tsaye number wayarsa nemo, a wannan ga'bar dole itama tayi wani k'okorin domin samun cikar muradin ta, bata iya k'arya ba amma tana ganin yau zata fara saboda abubuwan da Uwale da ita Gimbiyar suke mata a gidan sun isheta.

Murya na rawa kamar me shirin fashewa da kuka duk ta sheda masa abunda yake faruwa bata

tsaya a haka ba, sai da ta kara gishiri kamar yanda ta tsara hakan a ranta.

Yace." Hamra'u banyi mamakin jin wannan al'amarin ba, domin duk abinda akace min yarinyar ta aikata ba zan karyata ba, saboda dama can bata da tarbiya, to amma duk abinda za tayi ya tsaya iyakacin kaina domin ni na ajiye ta a gidan, ba zan lamunci taci zarafin wata daga cikinku ba, Mussaman Uwale da bani da kamarta a duniya , saboda haka kiyi hakuri idan na dawo zanyi wa tufkar hanci, na roki alfarma a gurinki cewa duk irin rashin arzikin da za tayi miki kada ki biye mata, ai kin fita nutsuwa da hankali da kuma ilimin addini, banda jahili babu wanda yake da ta'kidin cin zarafin dan adam wanda Ubangiji ya karrama shi a cikin hallita, mulki! izzah! iko! sune suke damunta da sannu ni zan sauke mata duk wani abu dake kanta."

Sassauta murya tayi cikin kissa gami da kokarin kar yaga laifinta tace." Insha Allahu zan kiyaye duk abunda za tayi min koda zata zagi iyayena ne to ba zan tanka mata ba, zan bari ne har ka dawo."

Yace." Yawwa nagode sosai my lov dina, maganar hidimar da Uwale take mata kada ki kara magana akai ki kyaleta tunda tana ganin zata iya idan na dawo dole ta ajiye aikin ta zauna ta huta."

Tace." To shikkenan Yaya na Allah ya dawo da kai lafiya."

Ya amsa da ameen ya Allah, kafin suyi sallama da juna.

******

Bayan kwana biyar da faruwar al'amarin, Asp ya kira ta a waya suka gaisa da juna ya tambayata ko tana da matsala tace babu, sai yace." To masha Allah haka ake so, ai mutumin naki yana kan hanya gobe mybe iwar haka ya sauka, ko da yake ma ai nasan ya fada miki dawowar tasa.

Gabanta yana d'an faduwa Tace." Aa ni bai fada min ba." Kawai ta tsinci kanta da fadin." Yaushe rabon ma da ya kira ni a waya."

Asp din ya shiga mamaki mutuka, kafin yace." Kinga kullum kuwa muna waya dashi kuma idan na tambayashi cewa kuna waya sai yace min Eh amma kiyi hakuri kada ki damu mybe aiki ne yay masa yawa.

Ta danne bacin ran dake taso mata tace." Ranka ya dade abokinka mak'aryaci ne, kuma bashi da kirki wallahi, ai ya san abinda ya aikata dole ya kare kansa a gurinka.

Yace." ZINATU ki daina jifan sa da irin wannan kalaman mijinki ne fa a koda yaushe ya zama magana mai kyau ce zata fito daga bakinki.

"Humm kawai ta iya cewa ranta idan yayi dubu ya baci Tace." Ba ka tambayi dalilin komai ba ka nema ka dora min laifi idan nace maka kana tsoronsa sai kace ba haka bane."

Yar dariya yayi yace." Ai na san labarin gizo ba zai wuce na koki ba, shiyasa ban tambayi dalili ba, amma dai ki fada min laifin da yay miki ina sauraranki."

Tace."Gabad'aya ya sanya an fita da kayan masarufin da masarautar mahaifina ta bashi, a cewarsa yafi karfin komai baya bukatar taimakon wani, shine ni kuma nai mamakin hakan nace har yaushe yayi arzikin da zai dinga yiwa mutane tutiya shin wai nawa ne ma albashinsa a wata."?

Asp din ya dinga jinjina maganar a ransa, ba tun yau ba yasan da cewar yarinyar ga'buwa ce zata iya farfada masa wannan maganganun.

Ya sauke ajiyar zuciya da fadin." Aa kece dai ki ka fahimceshi a bai-bai amma ba nufinsa kenan ba, domin mun jima da yin wannan maganar in da yake sheda min cewa akwashe kayan a rabawa mabukata, ba wai don baya bukata ba, tunda akwai wa'inda suka fishi bukata a raba musu sai a bar masa kadan, ni kaina yayi min kyautar wasu, nace A'a saboda nima Allah ya rufa min asiri, wannan shine dalilinsa, amma ina fatan bakiyi masa rashin kunya ba."

Shuru tayi masa domin shi kansa a yanzu haushinsa takeji ganin har yanzu yaki hango laifin abokin nasa .

Jin tayi shuru yasa ya gazgata zarginsa, yace." shikkenan shurunki ya bani amsa ba, kinga kuwa duk wani abu da yay miki a yanzu ke kika janyo amma bari zan kira shi yanzu domin naji komai daga bakinsa."

Still ba tace masa komai ba har ya gaji ya kashe wayarsa, zazzafar ajiyar zuciya ta sauke tare da cire wayar daga kunnata. ta a jiye saman drowar, kwanciya tayi ta lumshe idonta kawai ta shiga tunanin abinda zai faru a tsakaninsu idan ya dawo gidan.

Koda Asp din ya kira shi cikin mutumci da dattako suka gaisa kamar koda yashe, Asp din ya tambayeshi yanayin aikin da kuma maganar dawowarshi gobe, yace." Na kammala komai cikin nasara da sahalewar ubangiji kuma insha Allah gobe iwar haka na sauka da ikon Ubangiji.

Yace." Alhamdullhi masha Allah, mutumina na taya ka murna da samun cigaba a rayuwa Allah kuma ya sauke ka lafiya."

Cikin farin ciki ya amsa da ameen ya Allah mutumin kirki nagode kwarai."

Yace." A babu komai fa abokina idan nai maka addua da fatan alkairi ai kamar kaina nayi wa sai dai kuma hanzari ba gudu ba, yanzu-yanzu na gama waya da mutuniyarka."

Jin abinda yace yasa ya d'ora idonsa kan agogon dake kafe a dakin, goma da rabi na dare, sai ya shiga mamakin dalilin da yasa ya kira ta acikin wannan daran, be yarda da abinda zuciyarsa take raya masa ba, yace." ta kawo maka 'kara ta kenan."?

Murmushi yay da fadin." Kwarai kuwa UMARU a gaskiya idan baka sauya halinka ba zamu 'bata domin ni yanzu gabadaya na daina ganin laifin yarinyar nan laifinka nake gani."

Cike da mamaki yace." Wannan ya nuna min cewar kana goyon bayan duk iskancin da take."

Yace." Ba nufi na kenan ba, na san abinda take bata kyautawa, to amma ni nafi yarda da cewa kaine kake janyo duk abunda yake faruwa me yasa ba zaka rarrasheta ba; me yasa ba zaka dinga tausasa harshenka gurin yi mata kalami ba? nasha fada maka cewa mata wasu irin hallita ne masu wuyar sha'ani amma daga ranar daka gane hallinsu to za kaji dadin zama dasu, domin suna da dadin sha'ani da kuma saukin hali, me yasa kai baka daukar shawara ne."?

Asp yana da 'kima da daraja a idonsa, wannan shine dalilin da yasa ya dinga tausar zuciyarsa kada ta tunzurashi aikata abinda zai janyo musu samun sa'bani da juna, bayan haka kuma wannan gantafalfalar yarinyar bata isa ta shiga tsakaninsa da amininsa ba, hakuri ya bawa zuciyarsa dake turari! gami da jin kishi-kishin Asp din domin haka kawai yake jin haushin kyakykyawar fahintar dake tsakaninsa da yarinyar wanda hakan ya janyo yazo yana gaya masa magana a kanta..........Ajiyar zuciya ya sauke da fadin."To Naji na dauki laifina domin a yanzu yanda kake a tunzure ko nayi maka bayani ba zaka fahinta ba, okey komai zai yi dai-dai kamar yanda kake so, zan kuma yi kokarin ganin na gyara kuskura na."

Asp din yace." Yawwa to ko kai fa mutumina, ni wallahi banga abin gudu a tattare da yarinyar nan ba, a ganina kai da kanka zaka sauya mata hallaya kada ka manta kuma bata da kowa a garin nan sai kai da family naka sai kuma mu da muke abokanan arziki."

A d'an tunzure yace." Asp maganar nan abar ta haka don Allah, nace naji na kar'bi laifi na zan gyara kuma shikkenan ko."?

Yace." Shine abinda nake bukata a tare da kai, ka dawo gida naga sauyi daga gareka."

Shuru yay masa yana jin wani irin abu na sukan zuciyarsa, a duk sanda Asp din yake nuna kulawarsa akan yarinyar yakan ji abun ya dame shi a ransa, sai yayi auziyya ya kori shaidan din dake kusa dashi tukkuna yake samun sassauci, shi kansa be san me yasa yake tsananin kishin

yarinyar ba.

*Kika futar min da littafi keda Allah!  ki ka karanta baki biya ba kema keda Allah!*

*#500via.....0542382124.....Binta umar gtbabk, idan kati zaki turo  kiyi min magana ta WhatsApp da wannan number.... 07084653262.....BINTA UMAR ABBALE*
[2/9, 7:01 AM] Matar Malam: _*GOJE!!🏹🐕‍🦺*_
_*Ya dawo!! ga Akuya ga kura!! tofah! 'ka'ka-'kara-'ka'ka-tsara!! A yanzu ne labarin zai fara....! Na jima ina rubuce-rubuce amma ban ta'ba rubuta littafin daya dauki hankalina irin wannan ba, dalili littafin yazo da sabon salon da ba'a ta'ba yin irinshi ba, bahaushe yace yabon kai jahilci 😃 a wannan ga'bar dole na jinjinawa kaina gurin rubuta littafin farauta ba tare dana shirya hakan ba, Tirk'ashi idan ana dara fidda uwa ake, shin wai ina labarin uban daba ne? ina nufin (mashekin daji) wanda Ubana UMARU ya samu nasarar sare masa hannu guda🙊 akwai badakala anan gaba.......GOJE🐕‍🦺🏹 ya dawo cike da nasarori masu yawa shin ya zaman auran su zai kasance da 'yar rigimarshi  wato GIMBIYA ZINATU, wanda Tun a daji suka fara son junansu amma dukkaninsu sun 'ki gazgata cewa suna son junansu😃   to zamu ga yanda game d'in nasu  zai kasance tare da boyayyan masoyinta😃  shin  a tsakanin waye zai saduda  kowa dai ba kanwar lasa bane..........! Domin samun damar shiga paid group....#500 0542382124.....Binta Umar gtbank. Idan kati za'a turo sai ayi min magana ta WhatsApp da wannan number...... 07084653262......BINTA UMAR ABBALE🍒*_

*61&62*
*GJSR*
Wayewar garin ranar da zai dawo tun safe gidan  ya fara cika da mutane yan uwa da abokan arziki  daga can garinsu,  yaran shi ma kaf sun hallara, jiran saukar sa kawai suke, hayaniyarsu har part d'inta,  ta dinga mamakin al'amarin, Baraka ce take shaida mata cewa ai ba'ki akayi a gidan,  kuma  da  alamar su mutanan k'auye ne, jim tayi tana nazarin  meye dalilin zuwansa, wani sashe na zuciyarta ya tunasar da ita cewa sun zo tarar d'an uwansu ne, kasancewar a cikinsu shike da kumbar susa shine dalilin da yasa suke tururubin zuwa gidanshi.

Tsaki taja a fili tace." Duk  inda d'an kauye yake sai ya nuna halin dabbanci." Ta kalli Barakan dake zaune a gefanta tace." Ki sheda musu cewar hayaniyarsu tayi yawa su rage."
Ta amsa kafin ta yun'kura ta mike  kai tsaye hanyar fita ta nufa.

Da yake a 'bangaran da  suke zaune  ba'kin suka sauka,  kai tsaye can ta nufa. aikuwa ta samesu sunyi kaca-kaca da guri sunci abinci duk sun zubar sai dirkar lemon roba suke da sun shanye sai su ajiye su dauki wani, lemo da ruwan kusan kwali biyar aka a je musu amma sun shanye saura kadan.
Sosai ta cika da mamakin yanda ta gansu mazan da mata sai hira suke suna shewa kowanne

rike da robar lemo a hannu.

Tayi musu sallama suka amsa tace." Dama sa'ko ne daga matar gidan wato Gimbiya Zinatu tace na sheda muku cewa hayaniyarku tayi yawa ku tak'aita."

Sai suka hada baki gurin fadin." To shikkenan amma dai mutum da bakinsa ai ba za'a ha nashi magana ba ko."?

Tace." Eh itama ba tace kuyi shuru ba cewa tayi ku rage hayaniya."

Wasu daga ciki suka amsa sauran kuwa shewa sukayi irin ta shakiyanci suka fara kuskus da yawa daga cikinsu mutanan 'Dayyiba ne wato mahaifyar Hamra'u, domin ita bata samu damar zuwa ba, sai ta tura wakilai domin dauko mata rahoto.

Tun kafin ya sauka ya samu labarin tarin jama'ar dake jiransa, sosai yay farin cikin hakan ya kuma dinga Allah-Allah ya sauka domin haduwa da 'yan uwansa wanda bashi da kamarsu.

Uwale da kanta ta jagorance su duk yawan su maza da mata suka nufi sashen Gimbiyar.

Suka cika falon duk girmansa ko wanne sai zare ido yake da kalle-kalle falon ya dumame da wani irin wari da tsami mara dadin ji!!

Marakissiya ce ta shiga ta shiga ta sheda mata cewa tana da baki.

Koda ta fito ta riske su jigum-jigum! a zaune ga tsami da hamami! ya cika mata falo, ranta yay masifar b'aci, toshe hanci tai ba tare da tace musu komai ba ta juya da sauri ta koma daki.................A gaggauce ta nufi toilet ta dinga kwara amai! wanda ta kasa tantance na meye, ta dai fi zargin warin data sha'ka ne.

A galabaice ta fito ta zauna kan Sofa tana mayar da numfashi, ita kanta ba ta ji dadin faruwar hakan ba, sai dai ba yanda za tayi ta iya zama a falon yana wannan uban warin!

Uwale kuwa kunyar duniya ce ta isheta ta kalle su suna zaune har yanzu sai dai akwai alamun 'bacin rai a tare da wasu mussaman Kawun sa wanda suke 'yan maza zir da mahaifinsa.

Ya kalleta da fadin." Uwale wannan yarinyar i ta ce matar UMARU."!

Tace." Eh ita ce kuyi hakuri da abunda ya faru.

Kawu Ado ya girgiza kansa rai a bace yace." Babu shakka albasa ba tayi halin ruwa, yanda muke jin labarin mahaifinta a duniya mutum mai nagarta da dattako,  bashi da nuna bambanci ko 'kyama ga al'ummah! yana da kyauta da sakin fuska, kowa nasa ne, tabbas da  yarinyar nan ta gaji halin mahaifinta to da ba zata tozarta dan adam ba, amma babu komai. saboda nagartar Mahaifinta za'a zauna da ita amma dole sai UMARU ya auri za'bin mu matar da zata girmama ta kuma mutunta mu."

Gabad'aya  suka amsa da fadin." 'Kwarai wannan  hukuncin shine dai-dai Kawu."

Ya mi'ke tare da basu Umarnin tashi su fita, gabadaya har ita Uwalen suka fita duk jikinsu a sa'bule.

Kai tsaye sashen Uwalan suka nufa kowanne da b'acin rai a fuskarsa, ganinsu a sa'bule babu karsashi! ya sanya Hamra'u murmushi dama ai ta san za'a yi haka, da kamar ta hana Uwale jagorantarsu saboda ta san hali, to amma hakan ma babu laifi sun ga halinta a zahiri a gaba sai su kiyaye.

To Asp da kanshi ya d'auko daga airport kai tsaye Headquarter 'yan sandan suka nufa, nan ya tarar da yanda abokan aikinshi da wakilan manyan manyan 'yan siyasan da sukayi dafifi gurin taron shi,  yaji dadin hakan sosai, ya saki fuska yana gaisawa da kowa, sai fatan alkairin suke masa yana amsawa da farin ciki a tare dashi, a zahiri yana ganin 'kauna tun  daga kan abokan aiki da kuma jama'ar gari.

A takaice suka tattauna da Commissioner kafin ya bashi hutu na sati daya, Asp yace." Ranka shi dade ango ne fa, ya kamata a bashi hutun wata guda ya huta sosai ya kuma ci angoncin sa a tsanake." Cike da barkwanci yake maganar.

Yana 'yar dariya ya kalleshi da fadin." *GOJE* kaji abinda abokinka yake cewa."

Murmushi yayi yana kallon Asp din yace."  Hutun wata daya yay min yawa sai kace mace na dingi zama a gida, ranka ya dade sati daya ya ishe ni."

Asp din yace." Okey shikkenan tunda kace haka amma nasan nan gaba da kanka zaka nemi hutun."

Dariya kawai yayi sam bai bawa maganar  muhimanci ba, a ganinsa babu yanda za'ayi ya dauki hutu na wata saboda wata mace.

Cike da wasa da dariya sukayi sallama da commissioner din wanda yayi kokarin danne bacin ransa,  domin ya tsani  wannan kusancin dake tsakaninsu.

Tun a mota Asp din ya kira ta ya sheda mata cewa ta shirya kar'bar angonta gashin suna tare

yanzu iso gidan."

Gabanta ne ya shiga fad'uwa, ta tashi zaune tana sa'ke-sa'ke, ba wai tsoron haduwa take dashi ba, kawai a jikinta takejin kamar akwai abinda zai faruwa a tsakaninta dashi.

Wanka tayi ta cancand'a ado turaruka masu dadin kamshi ta fesa a jikinta.

Sai dai tana fitowa falon tayi saurin toshe hancin ta, har yanzu akwai sauran wari da hamamin mutanan 'kauyen.

Baraka ta 'kwalawa kira da suke kicin suna aiki.......ta fito da sauri tare da risinawa, har yanzu hannunta na toshe da hancinta tace" Ki san duk dubarar da za kiyi wannan warin ya fitar min a falo." Tana gama maganarta ta koma cikin dakin.

Baraka ta dinga bunka turaran wuta sako da loko na falon tana hadawa da air freshener da turaran tsinke, amma ina warin daban kamshin turaran ma daban.

Motar tana parking yaran shi, da suke dakon! isowarsa suka mike tare da karnukansu! kafin kice kwabo gurin ya kacame! da bushe-bushe! gami da gangi mai taken sunansa!

Fitowarsa daga motar ta sanya karnukan wani irin haushi!! gabad'aya suka cika gurin kafin su zagaye shi sai koke-koke suke suna shanshana rigar jikinsa, da alama sun jima kewarsa...........

Gabad'aya jikinsa ne ya rikice! kafin kice kwabo gumi ya fara yanko masa daga kowace kusurwa ta jikinsa! ganin haka ya sanya yaran nashi cigaba da bushe-bushen suna masa kirari irin wanda suke masa.

Rigar jikinsa ya fara kokarin cirewa, Asp ya zuba masa ido yana mamakin abinda yake shirin faruwa...........Har singlet din dake ciki be bari ba duk ya cire ya mi'ka masa tare da rigar.

Ya kar'ba kawai yana kallon ikon Allah..................Ya kalli gabas! yamma! kudu! a rewa! kafin ya kurma wani irin ihu!!! wanda ya jima beyi irinshi ba, aikuwa gurin gabadaya sai da ya amsa!!! Ihun! sai da ya ziyarci cikin gidajen mutanan dake Barack din, Uwale ta zabura! ta mike tsaye da fadin." UMARU ya sauka domin ga alama nan.........Mazan ne suka fara turareniyar fita, su kuma matan suka cigaba da tsumayin shigowarsa.

Gabad'aya jikinsa ya bud'e Damtsan hannuwansa suka wani kumbura! jijiyoyi rad'od'o!! Sai wani irin motsi suke. tsigar jikinsa duk ta mike! gumi sai karyo masa yake daga kowace ga'ba ta jikinsa. ihun!! yake kafin ya fara yi wa kanshi kirari kamar haka.............!

*" Namiji uban maza!! UMARU! Uban UMARU!  d'aga Tanimu, Kandagarki kurmar dutse mugun makaganri sai kure! Naci dubu sai ceto! nayi tawa kuma  nayi ta wasu! Ni ne K'adangaran bakin tulu  mai maganin wani Takadiri!  guguwa! maganin barazana!  Namiji a cikin maza! UMARU mai masoya gabas! yamma! kudu! a rewa!!" Yana wani irin nishi yake  kirarin tare da dadura!  wuka!  a kowane sassah na jikinsa.*

Tun sa'ilin da ya fara ifece-ifecen! Asp din ya fito da wayarsa ya fara masa vedio sosai abun ya bashi sha'awa,  ya dinga masa vedio da hotona a lokacin da yake kai kawo a gurin yana ciccije! baki tare da gurzar jikinsa da kaifaffar wu'kar! da ya fizga a jikin yaron shi Alba.

Kawu Ado ne ya k'araso gurin da 'kyar ya samu nasarar rike hannunsa, sai ya fara kwantar masa da hankali yana shafa kirjinsa dake cike da gargasa...........Ya dinga sauka a hankali a hankali  amma har yanzu numfashinsa bai dai-dai ta ba.

Asp yayi serving din duk abunda ya d'auka ya mayar da wayar ajihunsa,  in da suke ya nufa, a hankali yasa hannu ya kar'bi kaifaffar wukar dake hannunsa, ya mik'awa Alban tare da bashi umarnin mayar da ita gidanta.

Numfashi da huci kawai yake fesarwa gabad'aya hancinsa duk ya bude gumi  shar'ban a saman karan hancin,  Asp din ya fara kokarin mayar masa da rigarsa, ya  daga masa hannu alamun ya bari.

Kawu Ado yace." Kyaleshi ya sarara tukkuna ai duk ranar da tsumin ya tashi mu kan rasa gane kanshi

Yace." Okey to idan hakane kuwa yana bukatar hutu bari kawai mu  shiga dashi cikin gidan."

Kawu Adon yace." Hakan shine maslaha.

Duk yana jin su  tsabar rashin nutsuwa ya ha nashi magana, babu abunda yake bukata a yanzu sai  haya'ki walau na Shisha ko na Sigari.

Jiki a masifar sanyaye ta saki labulan ta samu gefen gado ta zauna tana jin wani fad'uwar gaba! duk badakalar da take faruwa  faru a kan idonta,  domin itama tana  jin azababben ihun!  ta zabura! ta mike tsaye da farko gigicewa tayi ta shiga neman ma'boya  domin ba ta manta irin kicimilin wahalar da tasha a daji ba,  jin ihun!! yana kara karfi had'e da sambatu yasa ta gazgata cewa shine ya sauka a gidan.
Gabanta na wani irin bugawa taje ta zuge window da kyar ta d'age lalube, duk da akwai tazara mai tsayi hakan be ha nata hango cibad'idi'n  da yake faruwa a gurin ba.

Mamaki take sosai akan al'amarin sa, wane irin mutum ne mai taurin kai wanda wuk'a duk kaifin ta bata yanka shi, haka fa ya dinga yi a daji,  ta dinga kuka domin ita a ganinta wannan

kaikkafar wukar a take za tayi kisa amma ko gezau! idan yana dadurawa jikinsa har wani tsalle yake, gabadaya yanzu al'amarinsa tsoro yake bata.

Asp ne ya shiga dashi dakinsa ko'ina tsaf tsaf kamshi sai tashi yake wannan duk aikin Hamra'u ne, domin tun bayan tafiyarsa ba ta bar aikinta ba, duk bayan kwana uku take shigowa ta gyara ko'ina tasa turare.

Ya kalleshi da jajayen idanuwansa da suka rine sakamakon tashin tsumin jikinsa........"Bani Sigari." Ya fada tare da mika masa hannu.......Da yake Asp din ma ya dan busawa sa'i da lokaci shiyasa baya rabo da ita a jikinsa ko a motarsa sai ya shiga laluban jikinsa, babu ko kara d'aya, da sauri ya fita domin duba masa a cikin mota.

Kasa hakuri yay ya mike ya fara binkice dakin, *Shisha* ya dauka ya zauna kasan kafet ya fara tada hayaki, Asp ya shigo ya samu dakin ya turnuke bece masa komai ba ya zauna gefansa yana kallonsa.

Sai da ya tabbatar da cewar ya sha'ki hayakin ya ishe shi sannan ya ajiye, yana fesar da wanda yay saura a bakinsa.

Asp din ya kalleshi da fadin." Yanzu dai na tabbatar da cewar ka samu relief kamar yanda kake bukata."

Shuru yay na minti biyu kafin yace." Alhamdulillhi wanka zanyi na huta domin bana tsammamin zama da kowa a yanzu sai Allah ya kaimu gobe."

Yace." Hakan yana da kyau, yanda kayi wannan gumurzun nima zan so ka huta ka samu nutsuwa kafin wani abu ya biyo ba......Ya mike tsaye da fadin." Bari na shedawa Gimbiya cewa tazo ta had'a maka ruwan wanka ko."? Yana yar dariya ya kare maganar.

Kallonshi kawai yay yana mamakin furucinsa, shima Asp din be sake wata magana ba, ya kama hanyar fita yana amsa kiran da akayi masa a waya.

Duk da ya damu yin wankan amma sai ya kasa tashi domin yaje yayi, kawai ya zauna jiran zuwan yarinyar kamar yanda Asp din yace, amma shi a jikinshi yana ganin kamar hakan ba zai yiwu ba, kawai dai ya biyewa san zuciyarsa ne.

*#500via.....0542382124.....Binta umar gtbabk, idan kati zaki turo kiyi min magana ta

WhatsApp da wannan number.... 07084653262.....BINTA UMAR ABBALE*
[2/10, 4:06 PM] Matar Malam: *GSUR*
*63&64*

*ROMANTIC🙈*
Da 'kyar  da jibin goshi Asp din ta shawo kanta har  ta yarda da zuwa sashen angon nata.........Asp din ya cigaba da kwantar da murya yana rarrashinta tare da bata tabbacin cewa shi angon  nata ne yake bukatarta a kusa dashi yana kuma da kyau taje ta kula dashi kamar yanda sauran mata suke yi.

Ta kalleshi cikin rashin walwala tace." Ai shi ya kamata yazo guri na bani zan kai kaina ba, kamar yanda ka fada idan ya damu dani to ya tako kafarsa yazo inda nake."

Ya 'bata rai da fadin." Zinatu idan baki min wannan alfarmar ba to babu shakka zamu 'bata zanyi fushi dake irin wanda ban ta'ba yi ba, Zinatu kwata-kwata  bana sonki da wannan dabi'un kullum so nake  ki zama mace ta gari, bayan haka kuma shima  nai masa magana  akan abunda yake aikatawa  ya kar'bi laifinsa domin da bakina da nasa yayi min alkawarin gyara kuskuransa, saboda haka kema ki ajiye duk wata kiyayya da kike masa ki zauna lafiya dashi.

Jikinta ne yayi sanyi ganin yanda ransa ya ba'ci! Tabbas mutumin ya cancanta da  komai saboda mutumci da kuma hallacinsa, wannan dalilin ne ya sanya ta amince da Uzurinsa amma ba dan ranta yaso ba.

Tunda suka doshi sashen  gabanta yake wani irin faduwa ta rasa meye dalili.

Suka tsaya bakin kofar ya kalleta da fadin." Bisimillah ki shiga yana ciki ni dama munyi sallama dashi zan wuce gida yanzu."

Shuru kawai tai tana kallonsa.

Had'e fuskarsa yayi don kada ta kawo wasa yasa hannu ya bude mata kofar falon, da hannu yayi mata alamar ta shiga.

